**COURSE GUIDE**

# HAU113 SADARWA A HARSHEN HAUSA (HAUSA LANGUAGE AND COMMUNICATION)

**Course Team** Dr. Mustapha Ibrahim Garba (Course Writer) – FUD
Dr. Sabi'u Inuwa Fagge (Course Editor)-POLAC

**NATIONAL OPEN UNIƁERSITY OF NIGERIA**

© 2023 by NOUN Press
National Open University of Nigeria
Headquarters
University Village
Plot 91, Cadastral Zone
Nnamdi Azikiwe Expressway
Jabi, Abuja

Lagos Office
14/16 Ahmadu Bello Way
Victoria Island, Lagos

e-mail: centralinfo@nou.edu.ng
URL: www.nou.edu.ng

All rights reserved. No part of this book may be reproduced, in any form or by any means, without permission in writing from the publisher.

Printed 2022

ISBN: 978-978-058-835-9

# HAU113: HANYAR SADARWA A HARSHEN HAUSA

## Gabatarwa (Introduction)

Wannan kwas na HAU113, yana da muhimmanci wajen koyo da nazarin Hausa a matsayin fage na ilimi, musamman darasin da ya shafi hanyar sadarwa a harshen Hausa wadda ta ƙunshi garjiya da zamani. Darasin ya kawo cikakken bayanin yadda ake yin sadarwa ta gargajiya da kuma ta zamani a tsakanin al'ummar Hausawa. Har ila yau, darasin ya taɓo gaɓoɓin da ake amfani da su wajen isar da saƙo. Wannan ya haɗa da batutuwan da suka danganci sadarwa, musamman wadda ake yi ta amfani da sassan jiki da kuma wasu alamomi. Darasin ya fito da bayanai kan yadda Hausawa suke isar da saƙonninsu tun daga lokacin gargajiya zuwa yau, za mu gan su daki-daki.

An gabatar da darasin bisa tsari na rukuni kuma kowane rukuni ya ƙunshi kashe- kashe na batutuwa daban-daban da suka danganci sadarwa a harshen Hausa. A cikin darasin an zo da cikakken bayani kan zubi da tsarin kwas ɗin ta yadda ɗalibi zai naƙalce shi ba tare da fuskantar wata wahala ba. A ƙarshen kowane kashi an zo da tambayoyin auna fahimta kan batutuwan da aka gabatar ƙarƙashin kowane kashi. Fasalin tambayoyin da ɗalibi zai gani domin nazari kafin jarrabawa a ƙarshen karatu nuni suke yi kan abubuwan da aka koya wa ɗalibi a wannan kashi. Haka kuma an samar da dama ga ɗalibi yadda zai iya tuntuɓar malami domin ƙarin haske a duk lokacin da wani abu ya shige duhu.

## Manufar Kwas (Course Aim)

Domin kyautata karatu da nazari kowane kashi yana da tasa manufa bayan babbar manufar kwas ɗin ta gaba ɗaya da aka zo da ita a farkon darasi. Ke nan abin da ɗalibi zai yi domin sauƙaƙa karatunsu shi ne ya karanci kowace manufa da take haɗe da kowane kashi na darasi domin gane ciki da wajen darasin, ba tare da an samu matsala ba.
Idan ɗalibi ya kula da kyau, manyan darussan da suke tattare da wannan kwas suna da yawa, sai dai za a iya taƙaita su kamar haka:

- Harshen Hausa
- Bunƙasar harshen Hausa
- Abubuwan da ake amfani da su wajen sadarwa
- Hanyar sadarwa ta gargajiya
- Hanyar sadarwa ta zamani
- Sadarwa ta ɗaiɗaiku
- Sadarwa ta Jam'i

## Yadda Za A Nazarci Kwas (Working through the Course)

Domin ganin an fahimci wannan darasi da kyau an tsara darasin ta yadda ɗalibi zai iya jan ragamar karatun ba tare da tutsu mai yawa ba. An dai rarraba kwas ɗin zuwa rukuni 3 da yake ƙunshe da kashe-kashe masu biye da juna, kuma kowane kashi an gabatar da shi yadda ɗalibi zai ga dangantakarsa da ɗan'uwansa da ke biye. Saboda haka fahimtar darasin zai biyo karatun ta-natsu da ɗalibi zai yi wa darasin, ya kuma auna fahimtar ɗalibi ta yin amfani da tambayoyin da aka zo da su a ƙarshen darasi. Da yake kuma akwai aikin jinga da malami zai dinga bayarwa bayan kowane kashi na kwas, ɗalibi zai samu damar ganin fasalin yadda jarrabawa za ta kasance in an gama darasin baki ɗaya ba tare da ya dogara da malami ba a wannan lokaci. Ana fatan a kammala kwas ɗin cikin mako 15, wato kowane kashi a cikin mako guda.

Daga ƙarshe ɗalibi ya sani cewa idan yana nazarin kwas ɗin, malaman da zai riƙa tuntuɓa ba koyaushe za su kasance tare ba, saboda haka sai ɗalibi ya tsara jadawalin karatunsa ya dace da kowane kashi, ya kuma riƙa kai ziyara da leƙa abubuwan da malami ya bayyana masa domin ƙarin nazari don faɗaɗa sani da ƙarin haske.

Me ya kamata ɗalibi ya mayar da hankali a kai a lokacin gabatar da wannan darasi? Ɗalibi ya tabbata ya fahimci abubuwa kamar haka:

1. Wannan kwas ko darasi yana da rukuni 3 da kashi 14.
2. Kowane rukuni yana da kashi 4 ko 5 ko 6 har zuwa 7.
3. Kowane kashi yana da ɓangaren auna fahimta.
4. Kowane darasi ko kashi yana da amsa amsoshin auna fahinta.
5. Kowane darasi ko kashi yana tafe da manazarta da wasu ayyukan don ƙara nazari.

## Kashe-Kashe na Darasi / Kwas (Study Units)

A wannan kwas akwai rukuni 3 da kuma kashi 14, kowane kashi yana a matsayin mako guda ne na darasi, ke nan za a kamala shi cikin mako 15. Ana kuma fatan a amsa tambayoyin auna fahimta a ƙarshen kowane kashi, daga ƙarshe kuma a amsa tambayoyi na auna fahinta don ganin ko darasin ya zaunu da kyau.

Domin kyautata karatun kwas ɗin an haɗa da jerin littattafan da aka duba da wasu ayyukan da za a iya cewa suna da muhimmanci ga wannan kwasa ɗin, za su ƙara haske fiye da ƙima. Neman waɗannan littattafai da wasu irin sa a laburare zai inganta nazari da fahimtar kwas yadda ya kamata. Ke nan a shiga gonar ɗakin karatu a gida ko inda ake ajiye littattafai a kusa ko nesa zai inganta nazarin wannan kwas.

A kula da liƙau da ake sa wa a cikin kowane kashin darasi, za su taimaka wajen ƙara haske na nazarin kwas ɗin baki ɗaya, sai dai a tabbata liƙau ɗin suna aiki yadda ya kamata, kada a bari sai lokacin da ake buƙatar su, a laluba a ga ko suna aiki ko ba su aiki, wato dai a gwada komai kafin ƙarshen kwas ɗin.

**Auna Fahimta (Assignment)**

Shi wannan kwas na tsarin da ba ruwanka da malaminka ne, ko na tafi-da-gidanka, shi ya sa ake jarraba fahimtar karatu ta hanyoyi UKU, hanya ta farko ita ce ta auna fahimta a ƙarshen kowane kashin darasi, sannan kowane kashi a ƙarshe ya zo da jinga da za a ba wa ɗalibi. Sai daga ƙarshe a yi jarrabawar ƙarshen zangon karatu, wanda zai nuna an zo ƙarshen darasin.

Auna fahimtar da ake yi a ƙarshen kowane kashi za ta kasance ƙaramar jarrabawa ce, za ta zo da maki 30 daga cikin 100. Ke nan, ana buƙatar ɗalibi ya amsa tambayoyi uku inda za a zaɓi 2 su kasance su ke ɗauke da maki 30, maki 15 ga kowace tambaya. Sauran maki 70 za su zo ne a jarrabawar ƙarshen kwas.

Jarrabawa dai kamar kullum za a gabatar da ita ne daga gida, ita ma ba a cikin aji ba, kuma za ta kasance ta Intanet ne, ke nan ilimin na'ura mai ƙwaƙwalwa abu ne mai muhimmanci ga ɗalibi.

**JINGA (Tutor Marked Assignment)**

Jingar aji tamkar gwajin jarrabawa ne ga ɗalibi, saboda haka amsa jingar da ke ƙarshen kowane kashin darasi zai ba wa ɗalibi damar fahimtar yadda jarrabawar ƙarshe za ta kasance. Yana da kyau ɗalibi ya mayar da hankali domin amsa irin samfurin waɗannan tambayoyi, domin za su sauƙaƙa amsa tambayoyin jarrabawa a ƙarshen darasin baki ɗaya.

**Jarrabawar Ƙarshen Darasi (Final Eɗamination and Grading)**

Ita dai jarabawa ita ce hanyar da ake gane ko ɗalibi ya gane darasi ko kuma ya samu naƙasu a wani ɓangare, saboda haka tana ɗauke da kaso mafi tsoka na 70 cikin 100. Ba wani dabo a cikin wannan fasali domin ana ɗauko samfurin jarrabawar ne daga tambayoyin da aka dinga turawa na auna fahimta da kuma jinga. Ke nan mayar da hankali wajen amsa waɗannan tambayoyi a lokacin darasi zai rage zafin tambayoyin ƙarshen darasi.

**Ga fuskar yadda darasin zai kasance:**

**MAIN COURSE**

**CONTENTS**

**Rukuni Na Farko Harshen Hausawa………………… 1**

Kashi Na 1 Ma’anar Harshe……………………………. 1
Kashi Na 2 Hausa Da Hausawa………………………… 6
Kashi Na 3 Bunƙasar Harshen Hausa ………………….. 13
Kashi Na 4 Yaɗuwar Harshen Hausa…………………... 26

**Rukuni Na Biyu (2) Hanyoyin Sadarwar Hausa Ta Gargajiya I………………………… 34**

Kashi Na 1 Ma’anar sadarwa da irenta…………………. 34
Kashi Na 2 Sadarwa ta zane-zane………………………. 38
Kashi Na 3 Sadarwa ta kayan kiɗa……………………… 42
Kashi Na 4 Sadarwa ta amfani da sauti…………………. 46

**Rukuni Na Uku Sadarwa Gargajiya Ta Sassan Jiki………………………………….. 50**

Kashi Na 1 Sadarwa ta kai……………………………… 50
Kashi Na 2 Sadarwa ta baki…………………………….. 54
Kashi Na 3 Sadarwa ta hannu…………………………… 59
Kashi Na 4 Sadarwa ta ido……………………………… 64
Kashi Na 5 Hanyar Sadarwa Ta Haɗaka ……………….. 68

**Rukuni Na 4 Hanyoyin Sadarwa Ta Zamani ………… 73**

Kashi Na 1 Sadarwa ta Zamani ………………………… 73
Kashi Na 2 Muhimmancin Sadarwa…………………….. 79

## RUKUNI NA FARKO HARSHEN HAUSAWA

Kashi Na 1 Ma’anar Harshe
Kashi Na 2 Hausa Da Hausawa
Kashi Na 3 Bunƙasar Harshen Hausa
Kashi Na 4 Yaɗuwar Harshen Hausa

## KASHI NA ƊAYA (1): HARSHEN HAUSA

### Abubuwan da Suke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Ma’anar Harshe
1.4 Muhimmancin Harshe Ga Rayuwar Al’umma
Auna Fahimta
1.5 Taƙaitawa
1.6 Ma’anar wasu kalmomi
1.7 Manazarta Da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahinta

### 1.1 Gabatarwa

A wannan kashi za mu tattauna kan ma’anar harshe. Harshe wani muhimmin abu ne da ake yin amfani da shi wajen isar da saƙo daga wani zuwa wani, ko daga wani zuwa ko kuma daga wasu zuwa wasu. Rayuwar ɗan’adam gaba ɗaya an gina ta ne a kan isar da saƙo da kuma karɓar saƙo. Shi saƙo a tsari na halittar ɗan’adam yana zuwa a tsari na furuci. Wato, ɗan’adam yana furta magana don ya isar da wani saƙo. Wannan hanyar halittacciya ce, wato kowane ɗan’adam a kowace al’umma yana yin amfani da harshensa na uwa ko na farko ya isar da saƙo ta hanyar furuci. Harshe shi ne ya ba wa ɗan’adam damar rattaba tunaninsa, ko wani saƙo a kan takarda ko waninta don isar da shi wajen gina rayuwarsa da kyautata zamantakewa. Ya kamata ka sani cewa kowace al’umma ta duniya tana da harshen da take yin amfani da shi wajen isar da saƙo da fahimtar juna. Saboda haka yana da matuƙar muhimmanci ka fahimci abin da ake nufi da ‘harshe’. Ta hanyar amfani da harshe ne ɗan’adam yake iya adana tunaninsa ba tare da ya ɓace ba. Harshe kacokan shi ne tubalin ginin al’umma. Idan babu harshe to haƙiƙa babu al’umma. Harshe yana da matuƙar amfani ga rayuwar ɗan’adam, domin duk wani ci-gaba da ɗan’adam ya samu to ya samu ne a dalilin isar da saƙo ko sadarwa ta hanyar amfani da harshe. Yanzu sai ka biyo ni domin ka ji ma’anar harshe.

## 1.2 Manufa

A ƙarshen wannan kashi za ka fahimci:

- Abin da ake nufi da harshe.
- Dangantakar harshe da al'umma.
- Muhimmancin harshe ga rayuwar al'umma

## 1.3 Ma'anar Harshe

Da farko ya kamata ka san cewa idan na ce 'harshe' ina nufin harshen da ɗan'adam yake yin amfani da shi wajen sadarwa. Wannan shi yake nuni da cewa harshe shi ne tubalin ginin al'umma. Duk wata al'umma ta duniya tana da harshen da jama'arta suke yin amfani da shi wajen fahimtar juna a tsakaninsu. Babu wata al'umma da za a kira ta da sunan al'umma sannan a ce kuma ba ta da harshen kanta. Shi ya sa ya kamata ka ƙara sanin cewa akwai dangantaka ta jini da tsoka tsakanin harshe da al'umma. Al'umma ba ta wanzuwa sai da harshe. Ka ga akwai al'ummar Hausawa harshen da al'ummar suke yin amfani da shi ana kiran sa Hausa. Saboda haka harshen Hausa halittaccen harshe ne ba jama'a ne suka zauna suka ƙirƙire shi ba. Halittattun harsuna na duniya da ake danganta su da wata al'umma su ne kamar haka: Ingilishi da Jamusanci da Faransanci da Yarabanci da Igbanci da Fulatanci da Angasanci da Larabci da Suwahilanci da makamantansu. To me ake nufi da harshe? Masana da dama sun yi ƙoƙarin bayyana ma'anar harshe. Ga bayanin da Zarruƙ da Wasu suka bayar kamar haka:

Zarruƙ da Wasu (1986: 1) sun bayyana harshe da cewa "Harshe magana ke nan wadda ake ji a fahimta. Harshe shi ne abin da ya bambanta ɗan'adam da sauran dabbobi. Harshe a wurin ɗan'adam linzami ne na tunani. Sauran dabbobi sai dai su yi kuka, ko gurnani, ko haushi, ko haniniya, don su nuna fushinsu ko murnarsu, ko wuyarsu. Ko daɗinsu. Hatta aku, da yake iya kwaikwayon maganar ɗan'adam, yana yi ne ba tare da tunani ba". Ka ga a nan za ka fahimci cewa mutum kaɗai ne yake iya riya abu a zuciyarsa, ko ya gani da idanunsa ko ya ji da kunnuwansa, sannan ya furta da bakinsa. Wannan ne dalilin da ya sa Chomsky (1972) yake cewa ana yin nazarin harshe domin cewa shi harshe shi ne madubin tunanin ɗan'adam.

## 1.4 Muhimmancin Harshe Ga Rayuwar Al'umma

Kamar yadda aka kawo bayani kan harshe cewa, shi ne ginshiƙin samuwar al'umma, domin idan aka ce wannan al'umma ce to lallai za ka

ga tana da harshen da take sadarwa da shi. Wannan shi yake kara fito maka da dangantakar harshe da al'umma. Wannan dangantakar ta nuna cewa harshe yana taka muhimmiyar rawa wajen inganta rayuwar al'umma. Muhimmiyar rawar da harshe yake takawa ta haɗa da:

Bayanin da Zarruƙ da Wasu (1986: 1-2) ya ce kan muhimmancin harshe kamar haka, "Harshe shi ne maƙunshin ilimi da tarbiyya. Ra'ayoyin al'umma da hikimominsu da tarihinsu da abubuwan sonsu da na ƙinsu duka da harshe ake faɗar su da adana na adanawa, har a bar wa na baya abin gado. Ta haka a'umma take renon 'ya'yanta bisa kyawawan al'adunta da hanyoyinta na rayuwa". Saboda haka, ka ga harshe shi ne taskar ilimin al'umma da tarihinta kuma shi ne tafarkin koyar da ilimin da zai kawo ci-gaba a zamantakewar al'umma da bunƙasarta.

Sannan, da harshe ne ake koyar da duk wasu fannoni na ilimi kamar ilimin kimiyya da fasaha da aikin injiniya da na likita da na lauya da tattalin arziƙi da kimiyyar harshe da tarihi da kimiyyar siyasa da fasahar ƙere-ƙere da makamantansu.

Harshe ne yake kawo duk wata wayewa da ci-gaban rayuwar al'umma. Haka kuma, Harshe shi ne ya haifar da rubutu har aka iya rubuta abin da ake furtawa ana adanawa da kuma koyarwa. Ka ga kenan harshe shi kansa fage ne na ilimi. Domin mutum yakan koyi harshen wasu don ya ji daɗin yin mu'amala da su, ko kuma don ya fahimci ilimin da yake ƙunshe a cikin wannan harshe. Haka kuma mutum yakan koyi harshensa na uwa domin ya san ilimin da yake tattare a cikinsa. Misali, don ya san ilimin nahawunsa da tasarifinsa da tsarin sautinsa da makamantansu. A nan abin da nake son nuna maka shi ne harshe shi ne maƙunshin ilimi amma ba shi ne ilimin ba. Ka ga ai idan mutum ya zauna a wata ƙasa ya yi shekaru yana mu'amala da mutanen ƙasar zai iya jin harshen al'ummar, amma ka ga dole sai ya koyi ilimin kimiyya da fasaha da nahawu da adabi da wannan harshe. Ka ga wannan yana nuna maka cewa mutum zai iya koyon harshensa na uwa a matsayin wani fage na ilimi.

Da harshe ne ake iya fahimtar fasahohin da suka danganci al'umma. Akan gane waƙa da maganganun azanci da suka keɓanta ga al'umma ta hanyar yadda suke yin amfani da harshensu. Adabi a matsayinsa na madubin rayuwar al'umma harshe shi ne magwajinsa.

Waɗannan batutuwa da na bayyana maka su ne wasu daga cikin muhimmancin harshe. A dunƙule, za mu iya cewa harshe shi ne sadarwa gaba ɗaya, idan babu harshe a matsayin hanyar sadarwa to da al'umma ba ta kasance ba.

**Auna Fahimta na 1**

1. Me ake nufi da harshe?
2. Kawo Muhimmancin harshe ga Al'umma guda biyar (5).

## 1.5 Taƙaitawa

A wannan kashi na kawo maka bayanin ma'anar harshe da muhimmancinsa wajen inganta sadarwa. Dangane da muhimmancinsa na yi maka bayanin yadda harshe ya kasance madubin tunanin ɗan'adam da fifita ɗa'adam a kan sauran halittu. Harshe shi ne kaɗai da yake tabbatar da wanzuwar al'umma.

## 1.6 Ma'anar Wasu Muhimman Kalmomi

- Harshe - magana ke nan wadda ake ji a fahimta ko Harshe shi ne abin da ya bambanta
ɗan'adam da sauran dabbobi.

## 1.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bagari, D. M. (1986). *Bayanin Hausa: Jagora Ga Mai Koyon Ilimin Bayanin Harshe*. Rabat-MAROC: Imprimerie El Maarif Al Jadida.

Chomsky, N. (1972). *Language and Mind (enlarged edition)*. New York: Harcourt Brace Joɓanoɓich.

Galadanci, M. K. M. (1976). *An Introduction to Hausa Grammar*. Ikeja: Longman.

Jinju, M. H. (1999). *Rayayyen Nahawun Hausa*. Zaria: NNPC.

Sani, M. A. Z. (1999). *Tsarin Sauti da Nahawun Hausa*. Ibadan: Uniɓersity Press.

Sani, M. A. Z. (1999). *Siffofin Daidaitacciyar Hausa*. Kano: Benchmark Publishers Limited, 2009.

Tudun Wazirchi, A. G. I. (2009). *Mu San Kare-Karenmu*. Kano: Rurum Printing and Publishing Company.

Yakasai, S. A. (2012). *Jagoran Ilimin Walwalar Harshe*. Sokoto: Garkuwa Media Serɓices Limited.

Wurma, A. G. (2005). *Daidaitacciyar Hausa da Ƙa'idojin Rubutunta*. Kaduna: Olatunde Rasheed Printing Works.

Zarruk, M. R. da Wasu. (2010). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 1.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

### Amsoshin Auna Fahimta na 1

1 Me ake nufi da harshe?

i- Harshe magana ke nan wadda ake ji a fahimta.

ii- Harshe shi ne madubin tunanin ɗan'adam.

iii- Harshe' ina nufin harshen da ɗan'adam yake yin amfani da shi wajen sadarwa

2. Kawo Muhimmancin harshe ga Al'umma guda biyar (5).

i- Harshe shi ne taskar ilimin al'umma da tarihinta kuma shi ne tafarkin koyar da ilimin da zai kawo ci-gaba a zamantakewar al'umma da bunƙasarta.

ii- Harshe ne ake koyar da duk wasu fannoni na ilimi kamar ilimin kimiyya da fasaha da aikin injiniya da na likita da na lauya da tattalin arziƙi da kimiyyar harshe da tarihi da kimiyyar siyasa da fasahar ƙere-ƙere da makamantansu.

iii- Harshe shi ne maƙunshin ilimi da tarbiyya. Ra'ayoyin al'umma da hikimominsu da tarihinsu da abubuwan sonsu da na ƙinsu duka da harshe ake faɗar su da adana na adanawa, har a bar wa na baya abin gado.

iv- Harshe shi ne ya haifar da rubutu har aka iya rubuta abin da ake furtawa ana adanawa da kuma koyarwa.

v- Harshe ne yake kawo duk wata wayewa da ci-gaban rayuwar al'umma

## Kashi Na Biyu (2) Harshen Hausa Da Hausawa

### Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Harshen Hausa Da Hausawa
  2.3.1 Harshen Hausa
  2.3.2 Hausawa
  Auna fahinta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma’anar wasu kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahinta

### 2.1 Gabatarwa

A kashin da ya gabata an nuna cewa akwai alaƙa mai ƙarfi tsakanin harshe da kuma al’umma. Ka gane cewa harshe shi ne tubalin ginin al’umma. Wato, idan babu harshe ba za a samu al’umma ba. Abin da nake son na nuna maka shi ne harshe da masu magana da shi tamkar jini ne da tsoka. Shi ya sa a wannan kashi zan yi maka bayani kan Hausa da Hausawa. Ka ga Hausa dai shi ne harshen, Hausawa kuma su ne mutanen da suke yin amfani da Hausa. Wato Hausa a matsayin harshe yana taimakawa wajen raya al’ummar Hausa ko Hausawa. Wannan kashi zai kawo maka bayani kan Hausa a matsayin harshe da kuma Hausawa masu magana da harshen Hausa.

### 2.2 Manufa

A ƙarshen wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Bayani kan Hausa da ƙasar Hausa.
- Sanin yanayin harshen Hausa da Ƙasar Hausa.
- Bayyana Hausawa da makwabtansu

### 2.3 Hausa Da Hausawa

A wannan batu za mu kalli abubuwa guda biyu wato, harshen Hausa da kuma Hausawa.

### 2.3.1 Harshen Hausa

Tunda yake harshe shi ne tubalin ginin al'umma. Sai mu fara da fahimtar tambayar da take cewa, me ake nufi da Hausa? An samu bambancin ra'ayi game da kalmar Hausa. Misali, Zarruk da Wasu (1986: 6) sun bayyana 'Hausa' kamar haka "Kodayake can farko, akwai ƙabilar Hausa. Duk da haka a yanzu wannan suna ya zamana harshe, ba na ƙabila ba. Domin idan aka ce ƙabila, ana nufin al'umma mai asali ɗaya da yare ɗaya da ƙirar jiki kusan iri ɗaya da al'adu iri ɗaya da falsafa ko ra'ayin zaman duniya iri ɗaya. Bayan haka kowa cikin al'ummar zai riƙa alfaharin shi ɗan ƙabilar ne. Hausawa sukan ce su ƙabila ne. To amma idan ka matsa tambaya, za ka ji haifaffen ƙasar Hausa ya ce maka asalinsa shi Bafilatani ne, ko Babarbare ko Banupe ko Buzu ko dai ɗan wata ƙabila daban. Ga shi kuma a wannan ƙabilar bai san ko sannu ba. Bayan haka wannan kalmar *Hausa* a wurin Bahushe ma'anarta 'harshe'. Idan aka yi magana da wani harshen daban, Bahaushe yakan ce yana ji ana *wata Hausa*. Wato a nan ka ga Hausa sunan harshe ne ba na ƙabila. Al'ummomin da suka taru suke yin magana da wannan harshe su ne Hausawa". Idan ka bibiyi wannan bayani na Zarruk da Wasu (1986) za ka gane cewa harshen Hausa dai harshe ne, na masu yin magana da harshen kuma sunansu Hausawa.

Shi kuwa Amfani (2012: 4) cewa ya yi "Hausa harshe ne, kuma tana ɗaya daga cikin harsunan ɗan'adam waɗanda ake samu a nahiyar Afirka. A lissafin ko ƙididdiga irin ta masana ilimin kimiyyar harshe harshen Hausa yana cikin wani babban rukuni na kason harsunan duniya wanda ake kira *Afroasiatic*. Shi ma wannan babban rukuni yana da 'ya'ya kuma kowane ɗa, shi ma ƙaramin rukuni ne mai ɗauke da harsuna. Ƙaramin rukunin da Hausa ke cikinsa shi ake kira gidan harsunan *Cadi*. Wasu harsunan 'yan gidan Cadi, waɗanda 'yan'uwan Hausa ne, su ne Angas da Bole da Ron". Za mu iya nuna taswirar harsuna 'yan gidan Cadi kamar haka:

Bishiyar Harsunan Gidan Cadi

| Na Yammaci | | Na Biu-Mandara | | | Na Gabaci | | Na Masa |
|---|---|---|---|---|---|---|---|
| A | B | A | B | C | A | B | |
| Hausa | Bade | Tera | Kotoko | Gidar | Kera | Dangla | Masa |
| Bole | Warji | Bura | Musgu | | Somrai | Mukulu | |
| Angas | Saya | Higi | | | Lele | Sokoro | |
| Ron | | Mandara | | | | | |
| | | Matakam | | | | | |
| | | Sukur | | | | | |

(Newman, 1990: 2)

A wannan taswirar an kawo wasu misalai na harsunan da ake kira ‘yan gidan Cadi. Harsunan sun fi haka yawa sai ka duba aikin (Newman, 1990: 2-4) don samun ƙarin wasu harsunan ƙarƙashin kowane rukuni. Kuma ka fahimci cewa harshen Hausa ya faɗo cikin harsunan gidan Cadi na yamma rukuni na A.

Idan ka yi la’akari da bayanan da Amfani (2012) ya kawo ya nuna cewa Hausa dai harshe ne daga cikin harsunan ɗan’adam, ya kuma nuna rukuni da gidan da harshen yake a tsari na ilimin kimiyyar harshe. Wannan kashi zai tafi a kan cewa Hausa dai harshe ne na al’ummar da ake kira Hausawa. Kuma masana harshen Hausa sun yi bayanin cewa Hausa harshe ne mai dogon tarihi da daɗewa ana amfani da shi wajen sadarwa. Sani (2009: 1) ya bayyana cewa “Hausa harshe ne da ya fi kowanne bunƙasa a Afirka ta Yamma.

**2.3..2 Hausawa**

Da farko dai yana da kyau ka sani cewa idan aka yi la’akari da harsunan Afirka ta Yamma zan iya faɗa maka cewa Hausawa wato masu magana da harshen Hausa su ne al’umma mafi yawa a faɗin Afirka ta Yamma. Sani (2009: 1) ya bayyana cewa “Bincike ya gano cewa fiye da miliyan hamsin da bakwai ke amfani da Hausa a matsayin harshen farko a jihohin Arewacin Nijeriya da Jamhuriyar Nijar”. Ya ƙara da cewa, “fiye da miliyan talatin da shida ke amfani da Hausa a matsayin harshen hulɗa, ba a waɗannan wurare kaɗai ba kuwa har da Arewacin

Jamhuriyar Benin da Arewacin Togo da Arewacin Ghana da sauransu". Idan ka duba da kyau za ka ga cewa Sani (2009) ya yi wannan furuci ne shekara sha ɗaya da suka gabata, ka ga adadin yanzu ai ya ɗara wanda ya faɗa. Ala kullu halin dai Hausawa suna da yawa, yawan nasu kuma ya ɗaga darajar Hausa a ko'ina a faɗin duniya. To, Hausawa yaya suke ko kuma na ce waɗanne irin mutane ne? Yanzu sai ka saurara don jin amsar wannan tambaya.

Adamu (1978: 10) ya bayyana cewa "Irin abubuwan da Dr. Barth ya gani lokacin da ya taho daga Tassawa ya biyo ta Katsina ya nufi Kano a 1850, ya shaidar mana cewa, noma shi ne ƙusar tattalin arziƙi a ƙasar Hausa. Rahotonsa ya nuna cewa, duk inda mutum ya duba a wannan hanya da ya bi, babu daji, daga gona sai saura". Wannan yana nuna maka cewa Hausawa dai manoma ne, kuma suna martaba sana'ar noma. Kuma ana noma iri biyu ne; na abinci da na kasuwa. Ga dai gero ga dawa ga masara ga wake ga gyaɗa ga auduga ga taba ga sauran abubuwan masarufi, kamar su gwaza da dankali da nome. Bugu da ƙari, yawancin bishiyoyin da aka bari ko aka dasa a cikin gonakin na amfani ne, misalin tsamiya da kuka da ɗorawa da sauran irinsu. Haka Barth ya gani tun daga Katsina har Kano. Kuma tun kafin wannan zamanin an san Hausawa a kan safarar daddawa daga gari zuwa gari, ko ma daga ƙasa zuwa ƙasa. Bayan haka tsutsar nan da ke cin tsamiya, sukan yi tattalinta, don su riƙa samun zare wanda suke saƙa siliki da shi (Adamu, 1978: 10)".

Bayan haka kuma yawancin Hausawa suna kiwon dabbobi, kamar awaki da tumaki da shanu da kaji da agwagi. Kiwon a wurinsu kamar asusu ne, mutum yana riƙe da 'yan dabbobi, duk sa'ar da wata bukata ta samu a sayar da su.

Hausawa sun shahara a fagen kasuwanci da safarar haja zuwa wurare masu nisa. Kuma sun yi suna wajen kutsa kai zuwa wasu ƙasashe don yaɗa addini ko neman aiki. Kusan ma a ce Afirka tsawonta da faɗinta babu inda ba su buga ba. Tun ƙarni na goma sha ɗaya Hausawa ke hulɗa da ƙasashen Larabawa. Suna ƙetare hamadar rairayi ta Sahara, suna zuwa Magrib (wato Maroko da Aljeriya da Tunisiya) da Lubayya ko Turabulus (wato Libya). Kuma suna ƙetara Cadi zuwa Sudan da Masar da ƙasar Makka (Sa'udu Arebiya). Suna kai musu fatu da ƙiraga da bayi, su kuma suna sayo tufafi da makamai. Wajen kudu da yamma kuwa, Hausawa suna kutsa kai cikin ƙasar Yarabawa da Gwanja da Dagomba da Ashanti a Ghana. A nan babban abin safararsu shi ne goro da gishiri. Su kuma sukan kai musu kanwa.

Yawancin abincin Bahaushe kuwa, ana yin sa da gero ko dawa ne, sai kuma sauran abubuwan haɗawa da na marmari, kamar su wake da shinkafa da alkama da kayan rafi da sauransu.

Yawancin Hausawa Musulmi ne, saboda haka yawancin al’adunsu da suka shafi aure da haihuwa da mutuwa, duk sun ta’allaƙa da wannan addini. Sai ɗan abin da ba a rasa ba, na daga bin al’adun gargajiya, musamman a wajen Maguzawa. Haka kuma wajen mu’amala da iyaye ko dangi ko abokai, ko shugabanni ko maƙwabta ko wanin waɗannan, yawanci na Musulunci ne. Kazalika sha’anin sana’a da kasuwanci da neman aiki duk a jikin Musulunci suka rataya.

Can ainihi, sana’a da kasuwanci da neman ilimi suna bin gado ne. watau kowa yana bin wadda ya gada kaka da kakanni. Kuma idan mai sana’a ya shiga baƙon gari, zai je ya sauka a gidan abokan sana’arsa ne. In ma koyo ya zo yi, zai je gidan masu sana’ar gidansu ne. Saboda haka kusan kowace sana’a akwai sarkinta da makaɗanta da mawaƙanta kai har ma da wasu al’adu na masu yin ta da suka bambanta da na sauran jama’a.

Bauta da barance a wurin Bahaushe ba munanan abubuwa ba ne, musamman dangane da sha’anin koyon sana’a. Bawa yana fansar kansa ta hanyar sana’a. Kuma mai koyon sana’a yana yin barance a gidan mai koya masa ne. Irin wannan almajircin, ana kiransa bauta. Duk mai wata sana’a ko ɗan kasuwa ko malami, yana alfaharin a ce ga wasu sun koya a wurinsa har sun ƙasaita ko ma har sun fi shi. Su kuma duk irin muƙamin da suka samu, ba za su raina shi ba, za su riƙa yi masa ladabi. Tushen bayani: (Alhassan da Wasu, 1988:1-7).

**Auna Fahimta na 1**

1. Su wane ne Hausawa?
2. _________ ya kawo ya nuna cewa Hausa dai harshe ne daga cikin harsunan ɗan’adam, ya kuma nuna rukuni da gidan da harshen yake a tsari na ilimin kimiyyar harshe.

## 2.4 Taƙaitawa

A wannan kashi mun kawo maka bayani kan harshe Hausa. Mun kuma kawo maka bayanai waɗanda suke bayyana Hausawa. Sannan mun bayyana maku abincinsu da sana’o’insu da kuma yadda suke aiwatar da bautarsu.

## 2.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi

- *Cadi* - Ƙaramin rukuni ne da harshen Hausa ke cikinsa

## 2.6 Manazarta


Adamu, M. (1978). *The Hausa Factor in West African History*. London: Oɗford Uniɓersity Press.

Adamu, M. T. (1997). *Asalin Hausawa da Harshensu*. Kano: Ɗansarkin Kura Publishers.

Alhassan, H. da Wasu. (1988). *Zaman Hausawa*. Lagos: Islamic Publication Bureau.

Amfani, A. H. (2012). Hausa Da Hausawa: Jiya Da Yau Da Gobe. In Amfani, H.A, et al (eds.) *Champion of Hausa Cikin Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press.

Sani, M. A. Z. (2009). Siffofin Daidaitacciyar Hausa. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Tudun Wazirchi, A. G. I. (2009). *Mu San Kare-Karenmu*. Kano: Rurum Printing and Publishing Company.

Newman, P. (1990). Nominal and Ɓerbal Plurality in Chadic. Dordrecht: Foris Publication.

Zarruƙ R. da Wasu. (1986). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa*. Ibadan: Uniɓersity Press Limited.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**Amsoshin Auna Fahimta na 1**

1- Su wane ne Hausawa?

Hausawa wato masu magana da harshen Hausa su ne al'umma mafi yawa a faɗin Afirka ta Yamma. Sannan suna zaune a jihohin Arewacin Nijeriya da Jamhuriyar Nijar". Akwai kimanin mutane miliyan talatin da shida ke amfani da Hausa a matsayin harshen hulɗa, ba a waɗannan wurare kaɗai ba kuwa har da Arewacin Jamhuriyar Benin da Arewacin Togo da Arewacin Ghana da sauransu. Yawancin abincin Bahaushe kuwa, ana yin sa da gero ko dawa ne, sai kuma sauran abubuwan haɗawa da na marmari, kamar su wake da shinkafa da alkama da kayan rafi da sauransu.

Yawancin Hausawa Musulmi ne, saboda haka yawancin al'adunsu da suka shafi aure da haihuwa da mutuwa, duk sun ta'allaƙa da wannan addini. Sai ɗan abin da ba a rasa ba, na daga bin al'adun gargajiya, musamman a wajen Maguzawa. Haka kuma wajen mu'amala da iyaye ko dangi ko abokai, ko shugabanni ko maƙwabta ko wanin waɗannan, yawanci na Musulunci ne. Kazalika sha'anin sana'a da kasuwanci da neman aiki duk a jikin Musulunci suka rataya.

2- . _________ ya kawo ya nuna cewa Hausa dai harshe ne daga cikin harsunan ɗan'adam, ya kuma nuna rukuni da gidan da harshen yake a tsari na ilimin kimiyyar harshe.

- Amfani (2012)

## Kashi Na Uku Bunƙasar Harshen Hausa

### Abubuwan da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Bunƙasar Harshen Hausa
3.3.1 Hulɗa Da Ƙasashen Larabawa
3.3.1.1 Bunƙasar Hausa Cikin Ajami
3.3.2 Zuwan Turawa Ƙasar Hausa
3.3.2.1 Bunƙasar Hausa Cikin Rubutun Boko
Auna Fhinta
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma'anar wasu kalmomi
3.6 Manazarta
3.7 Amsoshin Auna Fahinta



### 3.1 Gabatarwa

A kashin da ya gabata mun tattauna kan Hausa da Hausawa. A wannan kashin kuwa za a yi maka bayani ne kan yadda harshen Hausa ya bunƙasa. Wato dai, wannan kashi zai mayar da hankali wajen fito da hanyoyi ko dalilai da suka haifar da bunƙasar harshen Hausa. Kowane harshe na ɗan'adam akwai hanyoyin da ya bi ya bunƙasa ko ya game ƙasashe. Harshen Hausa kamar yadda tarihi ya nuna ya samu bunƙasa ta hanya biyu ko dalili biyu, su ne rubutun Hausa ta fuskar 'ajami' da kuma rubutun 'boko'.

.



### 3.2 Manufar Darasi

A ƙarshen wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Kawo yadda harshen Hausa ya bunƙasa.
- Sanin yadda hulɗa tsakanin Larabawa da Hausawa ta haifar da bunƙasar Hausa cikin ajami.
- Bayyana zuwan Turawan mishan da na mulkin mallaka sun haifar da bunƙasar Hausa ta hanyar rubutun boko.

## 3.3 Bunƙasar Harshen Hausa

Idan muka duba tarihin ƙago rubutu a duniya, da yadda abubuwa suka fara, da bunƙasarsu za mu ga masana ba su nuna yadda Hausawa suke yin amfani da tsarin rubutu ba, kafin zuwan Larabawa da Turawa. Da alama hakan ya faru ne saboda harshan Hausa bai bunƙasa a duniya ba sai bayan zuwan Larabawa da Turawa, haka kuma harshen bai sami zama harshe mai cin gashin kansa a ƙa'idar rubutu ba da ayyukan hukuma sai da boko ya yi nisa ƙwarai. Sannan, kuma harshen bai da gogaggu kuma fitattun masana a wancan lokacin, ana ganin waɗannan dalilan ne suka sa ba a sami damar fito da tsarin rubutun harshen ba, wanda aka yi amfani da shi kafin bayyanar Larabawa da Turawa. Bunza (2002:14) ya nuna cewa "tsagar gargajiya, da take da sassaƙa wasu daɗaɗɗun al'adu ne na Bahaushe da suke ɗauke da wata ma'ana ta musamman, wadda ya kira da hanyar isar da saƙo ta zane-zane, watau alamomin da masana suka kira da rubutu. Bisa wannan ra'ayi za a iya cewa Hausawa suna da tsarin rubutu tun kafin zuwan tsarin abacada (abcd) na Latin sai dai kawai saboda dalilan da aka yi bayani a sama, ya sa ba a sami adanannun irin waɗancan zane-zane ba ko kuma bunƙasar hanyar ta yin rubutu ba.

Akwai manyan hanyoyi da suka shahara waɗanda masana suka yi rubuce-rubuce a kan su, waɗanda ake bi ana rubutun Hausa. Waɗananan hanyoyi su ne wasu masana tarihi suke nuna cewa an fara amfani da su wajen rubuta Hausa, wasu kuma na nuna cewa su ne dai hanyoyin da aka fara yin amfani da su wajen rubuta Hausa a tsarin rubutun *abacada* watau Latin. Waɗannan hanyoyi su ne; rubutun 'ajami' wanda ya samu a dalilin Musulunci da rubutun boko wanda ya samu dalilin zuwan Turawa. A halin yanzu akwai hanyoyi biyu ingantattu waɗanda ake bi ana rubuta Hausa. Waɗannan hanyoyi su ne rubutun 'ajami' da kuma rubutun 'boko'. Tunda wannan kashi ya ƙunshi bayani kan bunƙasar Hausa, to zai yi kyau a bi tarihin waɗannan hanyoyi biyu tare da kawo bayanan gudunmawar da kowace hanya ta bayar wajen haɓaka Hausa.

### 3.3.1 Hulɗa Da Ƙasashen Larabawa

Da farko dai, ya kamata ka sani cewa hulɗar cinikayya da ziyarce-ziyarce a tsakanin ƙasashen Larabawa da ƙasar Hausa ta daɗe sosai. Larabawa sun shigo Afrika ta yamma domin yaɗa addinin Musulunci a ƙarni na 7, kuma sun shigo Borno a tsakanin (1098-1150), da suka isa Borno, sai suka shiga yaɗa addinin Musulunci da koyar da ilimi. Daga cikin Larabawan wasu sun bazu, har ya zuwa ƙasar Hausa domin yaɗa addinin musulunci da koyar da ilimi a ɓangarori daban- daban. Muhimmin tasirin da aka samu a sakamakon hulɗoɗin tsakanin ƙasar Hausa da ƙasashen Larabawa shi ne samuwar addinin Musulunci da

ilimin fannoni da suka haɗa da; samuwar ɗinbin kalmomin Larabci cikin harshen Hausa, sannan kuma ga samuwar rubutun ajami. Duk waɗannan sun samu ne saboda ilmantarwa cikin karatu da rubutu da amsa fatawa da kuma faɗakarwa. Domin Musulunci addini ne da yake tafiya tare da wayar da kan al'umma, dan haka ne aka sami al'ummar Hausawa ta rabauta da ilmin karatu da rubutu a cikin haruffan Larabci.

Hausawa sun daɗe suna koyon ilmin Larabci, amma ba a rubuta harshen Hausa da shi ba, sai daga baya wasu malamai suka fara sarrafa harufan Larabci suna rubuta Hausa da su, hakan ya fara faruwa ne, tun lokacin da suke rubuta wasiƙa cikin Larabci daga wannan malami ko basarake zuwa wani, suka fara ƙago rubuta sunayen laƙabi inda ake haɗa shi da na yanka. A wancan lokacin idan za a rubuta sunan yanka ana ganin irin su a littattafan addinin sunayen irin 'Muhammadu" ko 'Abudllahi, amma wajen rubuta sunayen laƙabi irin su 'Rumfa' wanda yake laƙabi ne na sarkin Kano 'Muhammadu Rumfa'. Don haka, sai suka ƙago yadda za a rubuta sunan 'Rumfa' ta hanyar amfani da harrufun Larabci ta la'akari da tsarin sautin Hausa. A lokacin sun yi amfani da 'ra'un' a matsayin 'r' sai 'mimun' a matsayin 'm' sai 'fa'un' a matsayin 'f' da haka suka samar da sunan laƙabi na 'Rumfa', kuma daga irin wannan tsarin rubuta sunan laƙabi ne malamai suka ci-gaba da amfani da sautukun Larabci suna rubuta Hausa ta yin la'akari da sautuka masu kama da sautukan Hausa. Daga nan kuma, don a sauƙaƙa hanyar mayyazewa duk baƙaƙen Larabci an ba su wani irin lafazi mai jirwaye da lufazin Hausa. Saboda haka aka sami kalmomin Larabci da yawa da suke shiga na harshen Hausa. Haka kuma shi ya sa malamai da yawa suka tsunduma wajen amfani da waɗancan sautuka wajen rubuta harshen Hausa wanda aka fi sani da ajami.

### 3.3.1.1 Bunƙasar Hausa Cikin Ajami

Bunƙasar Hausa cikin rubutun ajami kamar yadda muka yi bayani ya samu ne bayan zuwan addinin Musulunci ƙasar Hausa. Tarihi ya bayyana cewa wajen ƙarni na goma sha uku zamanin sarkin Kano Naguji Ɗan Ɗariku wasu 'yan kasuwa, Larabawa da Wangarawa suka fara zuwa ƙasar Hausa da addinin Musulunci (Ibrahim, 1982). Abu na farko da za mu iya cewa ya bunƙasa rubutun ajami shi ne bunƙasar kasuwanci da cinikayya da fatauci tsakanin ƙasashen Larabawa da ƙasar Hausa. Haka ma zuwan Fulani daga Futa-Toro ƙasar Hausa lokacin sarkin Kano Yakubu (1452-1463) domin da'awa da yaɗa addinin Musulunci. Haka Musulunci ya ci-gaba da bunƙasa da shigowar shehunnan malamai garuruwan ƙasar Hausa. Wannan ya taimaka wajen bunƙasar rubutun ajami a tsakanin malamai da sarakunan ƙasar Hausa (don samun ƙarin bayani sai ka duba aikin Ibrahim, 1982).

Samuwar makarantun allo da na zaure sun taimaka matuƙa wajen bunƙasar rubutun ajami cikin Hausa. Tun daga ƙarni na goma sha biyar ake ta samun ƙaruwar makarantun allo da na zaure. Hakan ta faru ne saboda ci-gaba da zuwan Larabawa da malamai ƙasar Hausa. Wani dalilin da ya taimaka wajen bunƙasar rubutun ajami cikin Hausa shi ne gudunmawar da shehunnan ɗariku suka bayar wajen yaɗa addinin Musulunci da bunƙasar makarantun zaure. Shehunnan ɗariƙu, musamman ɗariƙar Ƙadiriyya da Tijjaniya sun taka rawar gani a ƙasar Hausa wajen yin amfani da rubutun ajamin Hausa. Duba aikin Sa'id (1978) don ƙarin bayani.

Bugu da ƙari, jihadin Shehu Usmanu Ɗanfodiyo ya ƙara bunƙasa rubutun ajami a duk faɗin ƙasar Hausa. A wannan lokaci hanyar da ta fi sauƙin sadarwa ita ce ta hanyar waƙa, don haka aka sami rubutattun waƙoƙi da yawa a wannan lokaci cikin ajamin Hausa da Larabci da kuma Fulatanci. Irin waɗannan waƙoƙi duk sun danganci addinin Musulunci da yabon ma'aiki.

Waɗannan su ne manyan dalilai da suka sa bunƙasar ajamin Hausa. Don ƙarin ilimi game da nazarin ajami cikin Hausa da yadda yake da yadda ake yin sa sai ka duba ayyukan Bosso (2010) da Sa'id (2011) da sauransu. Don haka, a nan za ka ga cewa malamai sun sarrafa baƙaƙe da wasulan Larabci wajen rubuta Hausa a fannoni da dama da suka haɗa da; waƙoƙi da labarai da sauran fannonin ilimi daban-daban.

### 3.3.2 Zuwan Turawa Ƙasar Hausa

An fara rubuta Hausa cikin tsarin rubutun boko bayan haɗuwar Turawa da Hausawa. Rubutun boko yana ɗaya daga cikin ire-iren rubutu na duniya da aka rattaba tsare-tsarensu bisa tsarin abacada (abcd), waɗanda suka samo asali daga rubutun Latin. Kusan duk mutanen ƙasashen Turai, misali Ingila da Faransa da Jamus da Portugal da Denmark da sauransu, irin wannan hanyar rubutun suke bi a duk makarantunsu da littattafansu da harkokinsu na sadarwa. Saboda haka, tun da yake irin wannan rubutu suke yin amfani da shi, to duk al'ummar da suka haɗu da ita, irinta suke yin amfani da ita wajen bayyana labaran da suka shafi wannan al'umma, kamar abin da ya shafi rayuwarsu da wuraren zamansu da tsarin harshensu.

Turawa sun daɗe ba su sami labarin ƙasashen Afirka ba, sai daga baya a irin rubuce-rubucen da wasu suka yi inda suka ambaci wasu garuruwan da ke yankin Afirka irin waɗannan mutane sun haɗa da; Al-Hassan Ibn Muhammad Al-wzas Al-Fasi wanda ya rubuta littafi mai suna *Leo Africanus* a lokacin yana zaman kurkuku a ƙasar Italiya, a littafin ya ambaci sunayen wasu garuruwan a ƙasar Hausa, wannan ya haska wa Turawa, wanda daga nan suka fara shirin shiga Afirka. Waɗannan

Turawa masu yawon gano Afirka hankalinsu ya fi ga fahimtar labarin ƙasa, amma duk da haka akwai wasu da suke rubuta waɗansu bayanai game da wasu harsuna na Afirka.

Masana na hasashen cewa a ƙasar Denmark ne aka fara rubuta kalmomin Hausa cikin rubutun boko tun a ƙarni na 18. A cikin shekarar 1973 sarkin Denmark ya tura wakilai zuwa ƙasar Larabawa don gudanar da binciken kimiyya, amma mutum ɗaya ne ya rayu mai suna B.G. Niebuhr, wanda ya rubuta littafi na tsarin Larabcin ƙasar Yemen. A cikin shekarar wani mutumin Tunis mai suna Abdurahaman ya kai ziyarar jakadanci ƙasar Denmark tare da wani bawansa mutumin Borno wanda yake magana da Barbarci, da Larabci, da Hausa. A lokacin Neibur ya zama tafinta tsakanin sarkin Denmark da Abdurrahaman saboda, Neibur ya koyi Larabaci a tafiyar da suka yi, a sanadiyar haka, sai abota ta ƙullu tsakanin Neibuhr da Abdurrahman, har Neibuhr ya yi sha'awar koyon harshen Hausa da Barbarci daga bawan Abdurrahaman, ya duƙufa yana koyon Hausa, ta hanyar koyon sunayen abubuwa yana rubutawa gwargwadon yadda ya ji muryar kalmomin tare da fassara kamar haka:

| | Yadda ya rubuta | Yana nufin | Ma'ana |
|---|---|---|---|
| 1a. | Dudsji | dutse | hill |
| b. | koroma | ƙorama | stream |
| c. | crua | ruwa | water |
| d. | daua | dawa | guinea-corn |
| e. | sinkaffer | shinkafa | rice |
| f. | motum | mutum | man |
| g. | berni | birni | town |

An buga waɗannan kalmomi da waɗansunsu a cikin littafi mai suna *Life of Neibuhr* a Denmark shekarar 1791 (duba aikin Yahaya, 1988: 72-75 don ƙarin bayani).

A cikin Turawan da suka fantsama don gano Afirka a farkon ƙarni na 19 waɗanda suka yi rubuce-rubuce game da harshen Hausa akwai Henrich Barth da John Frederick Schon. Henrich Barth Bajamushe ne, wanda aka danƙa wa ragamar gano ƙasashen Afirka a tsakanin shekarar 1850 zuwa 1855 a lokacin ya yi bincike-bincike ta fuskar asali da muhalli da harsunan Afirka. Henrich Barth ya sayi wasu bayi guda byu, ɗaya ana ƙiransa Dorugu ɗaya kuma Abegga, sun zamar masa 'yan jagora, suna kuma koya masa Hausa. Bayan ya koma Ingila sai ya bar aikin, ya zauna wuri ɗaya ya rubuta littattafai waɗanda suka haɗa da:

- Traɓel and Discoɓeries in North and central Africa.
- Collection of ɓocabularies of central African language.

Shi kuwa J. F. Schon shi ne Baturen da ake kira da gwarzo a fagen rubuce-rubucen cikin Hausa a Turai a ƙarni na 20. Wasu daga littattafan da ya rubuta bayan yawace-yawace da nazarce-nazarce da ayyukan da ya yi na daidaita rubutun Hausa da ƙirƙiro da wasu alamomi a rubutun Hausa sun haɗa da:

- Dictionary of the Hausa language.
- Labari nagari
- Africa-proɓerbs, tales and Historical fragments (Hausa teɗts).
- Grammar of the Hausa language.

Sauran Turawan da suka yi rubuce-rubuce a kan Hausa kafin ƙarni na 20 zuwa farkon ƙarni na 20 sun haɗa da: Dr. William Baikie, da C.H. Robinson; Da Francis W. Newmaan; da C.E.J. Whiting da Sauransu. Bayan ci-gaba da Turawa suka yi da nazarin ɓangarori daban-daban na harshen Hausa a ƙarni na 20 an sami gagarumin ci-gaba wajen samuwar rubutun Hausa a tsarin abacada (abcd) watau tsarin Latin. Don haka, Turawa da yawa sun yi rubuce-rubuce cikin Hausa, kaɗan daga cikin waɗannan Turawa su ne: Hanns Ɓischer (Ɗan Hausa) da R.M. East da G.P. Bargery da R.C. Abraham da N. Skinner da P. Newman da R.G. Schuh da sauransu.

### 3.3.2.1 Bunƙasar Hausa Cikin Rubutun Boko

An buɗe makarantar elemantare ta farko a Kano wada ake kira makarantar ɗan Hausa a shekarar 1909 don koyar da ilmin zamani. Haka kuma, a tsakanin shekarar 1914 zuwa 1919 an buɗe ƙarin makarantu a wurare da dama a cikin jihar Arewa. Bayan makarantu sun samu a wurare daban-daban, wata matsala da ta addabi makarantun ita ce rashin littattafan karantawa. Saboda babu tsayayyun littattafan da aka rubuta da boko, musamma waɗanda aka tsara don koyarwa a ƙasar Hausa. Mafi yawan rubuce-rubucen da Turawa suka yi a cikin Hausa sun tsara su ne don koyar da Turawa a ƙasashensu. Amma a ƙasar Hausa duk littattafan da ake da su na Larabci ne, sai kuma rubuce-rubucen da aka yi cikin Hausa da rubutun ajami, waɗanda mafi yawansu waƙoƙi ne. A sakamakon haka ne aka yi yinƙurin samar da litattafan da za a yi amfani da su wajen koyar da 'yan ƙasa, watau samar da littattafan Hausa. Don haka, sai aka yi tsare-tsare a lokuta daban-daban don cimma wannan burin, wasu daga cikin tsare-tsaren sun haɗa da:

- Kafa Hukumar Fassara
- Kafa Hukumar Talifi
- Kafa Kamfanin Gaskiya
- Kafa Hukumar NORLA
- Kafa Kamfanin Littattafai na NNPC

**Kafa Hukumar Fassara**

Ganin cewa makarantun ilimin zamani (boko) sun fara yawa a wurare daban-daban na jihar Arewa, amma suna fama da matsalar ƙarancin littattafan koyarwa, sai Gwamnati ta kafa Hukumar Fassara mai suna *Translation Bureau* ƙarƙashin jagorancin Mr. C. E. J. Whitting a shekarar 1929 a Kano, sai kuma daga baya aka mayar da ofishinta na dindindin a Zariya a shekarar 1931. A shekarar 1932 aka miƙa shugabancinta hannun masanin Hausa, watau Dr. R. M. East (Skinner, 1980: 167).
Nauyin da aka ɗora wa wannnan hukuma ta fassara guda huɗu ne kamar haka:

- Fassara littattafai daga waɗansu harsuna kamar Larabci da Turanci zuwa Hausa.
- Wallafa littattafai cikin harshen Hausa.
- Shirya littattafai manya da ƙanana don karantawa a makarantu.
- Taimaka wa 'ya ƙasa su riƙa wallafa littattafai.

Hukumar fassara ta yi ayyuka da yawa, na fassara da wallafa littattafai, waɗanda aka yi amfani da su a makarantu, kuma har yanzu ana amfani da wasunsu. Kaɗan daga cikin littattafan da aka shirya a wannan hukuma sun haɗa da:

- Dare Dubu Da Ɗaya
- Labarun Hausawa Da Maƙ wabtansu
- Labaru Na Da Da Na yanzu
- Saiful Maluki
- Littafin Lissafi
- Al'amuran Duniya da Na Mutane
- Koyarwar Labarin Ƙasa da Tarihi
- Da sauransu

**Hukumar Talifi**

A shekarar 1933 an sauya sunan Hukumar Fassara ta koma Hukumar Talifi, watau *Literature Bureau*. Domin a faɗaɗa hukumar don a sami damar wallafa littattafai a cikin Hausa a kan fannoni daban-daban. Bayan an canza sunan hukumar, Daraktan ilimi na jihar Arewa, Hanns Ɓischer (Ɗan Hausa) ya ƙaddamar da wani shiri na gudanar da gasar rubuta ƙagaggun labarai don samar da litattafan hira na labarai a tsarin rubutun zube. An ɗora nauyin gudanar da wannan gasar ga Hukumar Talifi wadda Dr. R.M. East yake shugabanta. Don haka, ya yi sanarwa tare da bayar da ƙa'idojin gasar, kuma an sanya cewa duk wanda ya ƙago labari a rubuce za a karɓa a buga, kuma za a ba shi na goro. Wannan ya ja hankalin malamai da dama inda suka rubuta litattafai suka

aika domin shiga gasar. Daga ƙarshe an sami waɗanda suka yi nasara guda biyar kamar haka:

- Ruwan Bagaja na Malam Abubakar Imam
- Ganɗoki na Malam Bello Kagara
- Shaihu Umar na Malam Abubakar Tafawa Ɓalewa
- Idon Matambayi na Malam Muhammadu Gwarzo
- Jiki Magayi na Malam John Tafida da Dr. R.M. East

An buga waɗannan littattafai, kuma aka riƙa amfani da su a makarantu da kuma karantawa don nishaɗi. Muhimmin aikin wannan hukuma ta Talifi shi ne ta shirya littattafai da buga jarida.

**Kafa Kamfanin Gaskiya**

Da farko Hukumar Talifi ce take tsara duk littattafan da ake wallafawa, da kuma jaridar Nijeriya ta Arewa wadda ta koma *Gaskiya Ta Fi Kwobo*. Amma a kan buga mafi yawa a Ingila, wasu a Ikko (Lagos), wasu a maɗaba'ar gwamnati da take a Kaduna, wasu a *Niger Press* ta Jos, domin Hukumar Talifi ba ta da maɗaba'a ta kan ta. Saboda haka, domin neman sauƙi da hanzari sai Gwamnan Nijeriya na lokacin, Sir Arthur Richards ya nemi gwamnatin Ingila ta taimaka wa Hukumar Talifi da kuɗin sayan injinan buga littattafai da na gina kamfani. Gwamnatin Ingila ce ta taimaka da kuɗi aka kammala ginin *Gaskiya Corporation* da ke Zariya a shekarar 1945. Bayan samar da wannan kamfani ya zamo shi ne yake buga kusan duk littattafai da jaridun da ma'aikatan Hukumar Talifi suka tsara. Irin littattafan da aka buga sun haɗa da:

- Ka Koyi Karatu
- Ka Ƙara Karatu
- Ka Yi Ta Karatu
- Bala da Babiya
- Yawon duniyar Haji Baba
- Mungo Park Mabuɗin Kwara.

**Kafa Hukumar NORLA**

Yanzu kuma zan gabatar maka da batu a kan kafa Hukumar NORLA. Dalilin da ya haifar da kafa wannan hukuma shi ne sakamakon faɗin jihar Arewa, da yawan mutanenta, da buƙatuwarsu ga ilmin zamani, sai gwamnatin jihar Arewa ta yanke shawarar yin wani shiri na yaɗa ilmi ga manya da kuma haɓaka rubuce-rubuce don kowa ya sami abin karantawa. A shekarar 1953 gwamnatin Arewa ta kafa kwamitin yaƙi da jahilci, wanda aka ɗora wa alhakin duba hanyoyin da suka kamata a bi don cim ma burin yaɗa ilimin zamani, kwamitin ya kawo shawarwari kamar haka:

- Gudanar da azuzuwan koyarwa.

- Shirya littattafai cikin Hausar boko da kuma wasu manyan harsunan arewa.
- Koyar da Ingilishi.
- Tsara hotuna don koyar da ilmi a sauƙaƙe.

An yi yinƙuri sosai wajen gudanar da kowane ɗaya daga cikin manufofin da kwamitin yaƙi da jiahilci ya zayyana. Don haka, an buɗe azuzuwan yaƙi da jahilci a ko'ina, tare da naɗa jami'an yaƙi da jahilci a kowane lardi domin kula da shirin.

Hanya ta biyu da kwamitin ya kawo ita ce ta shirya littattafai cikin Hausa a rubutun boko da na ajami. Don haka, aka kafa Hukumar Samar da Adabi ta Jihar Arewa (North Regional Literature Agency) wadda ake taƙaitawa da NORLA, wannan hukuma ta fara tsara littattafai tare da buga su a shekarar 1954.

Ayyukan da aka yi a hukumar NORLA suna da yawa, musamman tsarawa da buga littattafai iri-iri a kan fannoni daban-daban, da jaridu da waƙoƙi da kalandoji da hotunan wayar da kai da sauransu. Wasu daga ire-iren littattafan da aka tsara kuma aka buga a wannan hukuma sun haɗa da:

- Hanyar Karatu
- Hanyar Rubutu
- Hanyar Lisssa
- Ajami da Boko
- Yadda ake Rubuta Wasiƙa
- Mu Koyi Hausa
- Mu Yaƙi Jahilci

**Da sauransu.**

Bugu da ƙari hukumar NORLA ta buga jaridu iri-iri waɗanda aka tsara don kowane Lardi na Jihar Arewa. Misali akwai jaridun da aka tsara aka buga a cikin harshen Hausa, waɗanda suka haɗa da:

| Sunan Jarida | | Lardi |
|---|---|---|
| Jakadiya | - | ko'ina |
| Alfijir | - | ko'ina |
| Abiki | - | don makarantu |
| Zaruma | - | Sokoto |
| Gamzaki | - | Filato |
| Himma | - | Katsina |
| Sodangi | - | Kano |
| Zumunta | - | Bauchi |
| Bazazzaga | - | Zazzau |
| Haske | - | Neja |

Wannan hukuma ta gudanar da ayyuka ta fuskar tsarawa da buga littattafai da jaridu a cikin harshen Hausa da sauran manyan harsunan jihar Arewa. Wata hanyar da ta taimaka wajen haɓaka rubutun boko ita ce kafa Kamfanin Samar da Littattafai na NNPC a Zariya. Yanzu sai ka biyo ni ka ji labarin.

**Kafa Kamfanin Littattafai na NNPC**

An kafa Kamfanin Littattafai na Nijeriya ta Arewa (Northern Nigerian Publishing Company Limited), watau NNPC a shekarar 1966, sakamakon ƙulla yarjejeniya tsakanin Gwamnatin jihar Arewa da wani kamfanin tallan littattafai na Ingila mai suna *Macmillan Publishers*. An ba wannan kamfani damar ya zaɓi duk littattafan da ya ga zai saya a cikin tsofaffin littattafan da aka buga a baya domin sabunta buga su. Bugu da ƙari, kamfanin NNPC yana karɓar rubuce-rubucen mawallafan Hausa, bisa yarjejeniya, su buga don haɓaka rubuce-rubucen Hausa. Baya ga littattafan da wannan kamfani ya buga a fannoni daban-daban, kamfanin ya gudanar da wata gasa ta wallafe-wallafen ƙagaggun labarai na Hausa, kamar yadda Hukumar Talifi ta yi a shekarar 1933. Don haka, marubuta da dama sun shiga gasar, daga ƙarshe aka zaɓi guda takwas aka yi musu kyauta. Daga cikin littattafan akwai:

- So Aljannar Duniya na Hafsat Abdulwahid
- Amadi na Malam Amah na Magaji Dambatta
- Mallakin zuciyata na Sulaiman I. Katsina.

Waɗannan hukumomi da aikace-aikacen da suka gudanar sun tallafa sosai wajen bunƙasar rubutun Hausa. Duk bayanan da na gabatar maka idan ka duba aikin Yahaya, (1988) duk za ka gan su har ma ka samu ƙarin bayani a game da su.

Don haka, wannan shi ne bayanin yadda Hausa ta bunƙasa ta hanyar rubutu da ta faro daga Larabawa da Turawa har ta kawo ga ‘yan ƙasa wato Hausawa (don samun cikakken bayanin abubuwan da na bayyana maka da wasu sai ka duba aikin Yahaya (1988). Bunƙasar Hausa ta waɗannan hanyoyi da ka ji bayaninsu daki-daki sun yi tasiri matuƙa a kan yadda aka yi amfani da Hausa a kafofin sadarwa kamar yadda za ka ji nan gaba.

**Auna Fahimta na 1**

1. Shin rubutun boko yana ɗaya daga cikin ire-iren rubutu na duniya da aka rattaba tsare- tsarensu bisa tsarin abacada (abcd), waɗanda suka samo asali daga rubutun Latin?
2. Kawo littattafan guda biyar da NORLA ya tsara kuma aka buga su.

## 3.4 Taƙaitawa

A wannan kashi ka fahimci cewa:

- Tarihin bunƙasar harshen Hausa ta fuskar rubutu.
- Ta hanyar hulɗa da ƙasashen Larabawa Hausa suka sami hanyar rubutun ajami.
- A dalilin zuwan Turawa kuma Hausa ta samu hanyar rubutu ta biyu da ake kira da rubutun boko.
- Turawa ne suka fara bunƙasa Hausa ta hanyar boko.
- Hausawa ne suka bunƙasa ajami cikin Hausa bayan zuwan addinin musulunci.
- Harshen Hausa ya bunƙasa ta hanyar kafa makarantun gwamnati na boko da hukumomi da kamfanoni da suka bayar da gudunmawa.
- Bunƙasar boko a ƙasar Hausa yana da alaƙa da zuwan Turawa da ayyukansu.
- Hukumomin da suka taka rawa wajen haɓakar rubutun boko sun ƙunshi zuwan kafa hukumar fassara da hukumar talifi da kamfanin gaskiya da hukumar NORLA da kamfanin samar da littattafai na NNPC.
- ‘Yan ƙasa sun bayar da gudunmawa ƙarƙashin hukumomin gwamnati.
- Samar da makarantun boko na ɗaya daga cikin ginshiƙan abubuwan da suka taka

## 3.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi

- Jakadiya – sunan Jarida ne da ake bugawa a ko’ina
- Ajami – tsarin rubutu ne da ake amfani da haruffan Larabci wajen rubutun Hausa

## 3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bosso, M. A. (2010). *Nazarin Ajami Cikin Hausa*. Minna: Hasbunallah Printers.

Bunza, A. M. (2002). *Rubutun Hausa: Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre LTD.

Ɗangambo, A. (1993). ‘Ƙa’idojin Rubutun Hausa: Matattakala Zuwa ga Harshen Ƙasa’. Cikin Rufa’i, A. da Yahaya, Y. da Bichi, A. (ed).

*Nazari Kan Harshe da Adabi da Al'adu na Hausa*. Littafi na Uku. Kano: Jami'ar Bayero.

Ibrahim, M. S. (1982). Dangantakar Al'ada da Addini: Tasirin Musulunci kan Rayuwar Hausawa. Kundin Digiri na Biyu, Jami'ar Bayero Kano.

Mahmoud, I. (2001). *Ƙa'idojin Rubutun Hausa: Don Ɗalibai da Marubuta da Masu Nazari*. Kano: Ahmadu Publishing Network. Muhammad, D. (1990). *Hausa Metalanguage*. Ɓol I. Ibadan: Uniɓersity Press Limited.

Peɓret, Ɗ. (1995). *The Written World in UNESCO COURIER* (the origin of writing). Paris. UNESCO.

Sa'id, B. (1978). Gudunmawar Masu Jihadi kan Adabin Hausa. Kundin Digiri na Biyu, Jami'ar Bayero Kano.

Sa'id, B. (2004). *Ƙa'idoji-Rubutun Hausa: Jagora ga Marubuta*. Kano: Benchmark Publisher Limited.

Sa'id, B. (2011). *Daidaita hanyar Rubutun Ajamin Hausa Da Inganta Shi*. Kano: Gidan Dabino Publishers.

Skinner, N. (1980). *An Anthology of Hausa Literature*. Zaria, NNPC, 1980.

Wurma, A. G. (2005). *Daidaitacciyar Hausa da Ƙa'idojin Rubutunta*. Kaduna: Olatunde Rasheed Printing Works.

Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa a Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Zaria: NNPC.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**Amsoshin Auna Fahimta**

1. Shin rubutun boko yana ɗaya daga cikin ire-iren rubutu na duniya da aka rattaba tsare- tsarensu bisa tsarin abacada (abcd), waɗanda suka samo asali daga rubutun Latin.

- Haka ne

2. Kawo littattafan guda biyar da NORLA ya tsara kuma aka buga su.

- Hanyar Karatu
- Hanyar Rubutu
- Hanyar Lisssa
- Ajami da Boko
- Yadda ake Rubuta Wasiƙa
- Mu Koyi Hausa
- Mu Yaƙi Jahilci

## Kashi Na Huɗu Yaɗuwar Harshen Hausa

**Abubuwan da Suke Ciki**

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Yaɗuwar Harshen Hausa
 4.3.1 Dalilan Yaɗuwar Harshen Hausa
 Auna Fhinta
4.4 Taƙaitawa
4.5 Ma'anar wasu kalmomi
4.6 Mnazarta
4.7 Amsoshin Auna Fahinta

## 4.1 Gabatarwa

Wannan kashi an yi bayani a kan yaɗuwar harshen Hausa. Ka fahimci cewa 'yaɗo' ya bambanta da 'bunƙasa'. A kashin da ya gabata na yi maka bayani kan bunƙasar harshen Hausa. Wato ka fahimci hanyoyin da suka taimaka Hausa ta haɓaka. Wannan shi ne abin da ake nufi da 'bunƙasa'. 'Yaɗo' kuwa ya danganci yadda harshe yake samun ƙaruwar masu magana da harshe waɗanda tun farko ba 'yan asalin harshen ba ne. Ka ga wannan ma'ana tana nuna maka cewa bayan harshe ya bunƙasa zai iya kuma yaɗuwa ya kai ga wasu ƙasashe ko garuruwa da ba na asalin masu magana da harshen ba. Wannan kashi zai yi maka bayani kan yaɗuwar harshen Hausa. Harshe ba ya yaɗuwa sai da dalilai. Waɗannan dalilai wannan kashi zai bi don ya nuna maka yadda harshen Hausa ya yaɗu. Ya kamata ka sani cewa kowane harshe yana da irin nasa hanyoyin da suka kai ga yaɗuwar harshen. Harshe yana yaɗuwa ne ta yin la'akari da su masu magana da harshen. Ka ga za mu iya cewa yaɗuwar harshen Hausa ya ta'allaƙa da yanayin Hausawa. Yanzu sai ka biyo ni don ka ji abubuwan da suka haifar da yaɗuwar Hausa zuwa wurare da ƙasashe daban-daban.

## 4.2 Manufar Darasi

A ƙarshen wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Bayanin yadda harshen Hausa ya yaɗu zuwa wasu ƙasashe ko garuruwa.
- Kawo dalilan da suka haifar da yaɗuwar harshen Hausa.

## 4.3 Yaɗuwar Harshen Hausa

Kamar yadda muka yi maka bayani a baya, yaɗuwar harshe ya danganci ƙaruwar yawan masu magana da harshe waɗanda asali ba masu magana da harshen ba ne. Irin wannan yaɗuwar tana faruwa bayan harshe ya bunƙasa ta hanyar rubutu. Ka ga harshen Hausa ya samu bunƙasa ta hanya biyu kamar yadda na gabatar maka a baya, wato hanyar boko da ta ajami. Hanyar boko ta fi ta ajami bunƙasa a dalilinTurawan mulkin mallaka da tsarin gwamnati na buɗe makarantun boko da samar da wasu cibiyoyi da suka tallafa wa ƙoƙarin gwamnati da na Turawan mulkin mallaka. Ka ga harshen Hausa ya samu bunƙasa, amma yaɗuwarsa haɗe take da su kansu Hausawa. To, ta wace hanya Hausawa suka taka rawa wajen yaɗuwar Hausa kuma waɗanne hanyoyi ne ko dalilai suka ƙara taimaka wa Hausawa wajen yaɗuwar Hausa. Yanzu sai ka biyo ni zuwa sashe na gaba don ka ji dalilan da suka haifar da yaɗuwar Hausa.

### 4.3.1 Dalilan Yaɗuwar Harshen Hausa

Dalilai da dama kan iya haifar da yaɗuwar harshe. Za ka ji ana cewa akwai Hausawa ko masu magana da harshen Hausa a ƙasashen Ghana da Mali da Libya da Senegal da Saliyo da Kamaru da Kongo da Sudan da sauransu. Abin tambaya a nan shi ne mai ya haifar da haka. Wannan ba abu ne da ya faru lokaci ɗaya ba, yana da dogon tarihi. Ko dai me ya faru, wani dalili ne ya kawo hakan. Wasu daga cikin dalilan da zan iya faɗa maka sun haifar da ƙarin yawan masu magana da Hausa sun haɗa da:

- zaman tare tsakanin al'ummu mabambanta
- fatauci
- ƙaura
- yawan masu magana da harshe
- yaƙe-yaƙe
- bunƙasar harshe

Yanzu za mu yi maku bayaninsu ɗaya bayan ɗaya.

- Cuɗanya Tsakanin Al'ummomi Mabambanta

  Cuɗanya tsakanin al'ummomi daban-daban yana haifar da ƙaruwar masu magana da harshe. Amma yaya hakan ke faruwa? Yayin da aka samu al'umma babba cikin ƙananan al'ummomi suke yin cuɗanya ta mu'amalar zaman tare kamar kasuwanci da addini da neman ilimi, to lallai za a samu matsala wajen yin amfani da harshen ƙananan al'ummomi. A irin wannan yanayi al'ummar da ta fi girma wajen yawan masu magana da harshe kan danne sauran harsunan ƙananan al'ummomin. Sai ya kasance idan an zo harkokin cuɗanya da juna sai jama'a su yi amfani da

harshen da mutane suka fi yi. Ka ga ta irin wannan hanya ko dalili sai a samu ƙaruwar masu magana da harshe. Haka harshen Hausa ya yi dangane da ƙananan harsunan da suke arewacin Nijeriya kamar a garuruwan Maiduguri da Jos da Kaduna da Bauchi da makamantansu. A waɗannan garuruwa da wasunsu suna yin amfani da Hausa wajen yin cuɗanya don yin kasuwanci ko neman ilimi ko a wasu harkokin na zamantakewa. Wannan dalili ya sa ana yawan amfani da harshen Hausa, saboda haka a kullum yaɗuwa yake ƙara yi, wato masu magana da harshe kullum ƙaruwa suke yi a wasu garuruwan da ba na Hausa ba. Ta haka ne sai ka ga Banupe yana jin Hausa raɗau

- **Fatauci**

  Fatauci ma wani dalili ne da ya haifar da yaɗuwar harshen Hausa. Hausawa an san su da harkar safara ko fatauci. Wato an san Bahaushe da cewa mutum ne wanda yake sayen kaya a wannan gari ya tafi wani garin ya sayar. Fatauci shi ya kai Hausawa garuruwa a arewacin Nijeriya kamar Makurɗi da Jos da Lakwaja da wasu garuruwan kudancin Nijeriya. Haka ma fatauci ne ya kai Hausawa wasu ƙasashen Afirka kamar Gwanja (wato Ghana) da Kamaru da Kwadibuwa da Benin da Dahomi da Sudan da Kongo da Libya da Gambiya da Senegal da sauransu. A irin waɗannan garuruwa Hausawa sukan daɗe ba su dawo gida ba, wannan ya sa sun yi aure a irin garuruwan ko ƙasashen da suke zuwa, kuma suna ci-gaba da amfani da Hausa. Abokan kasuwancin Hausawa sukan ji sha'awar koyon Hausa don samun sauƙin mu'amala ta kasuwanci. Harkar saye da sayarwa da Hausawa suka yi suna a kai ya haifar da yaɗuwar Hausa a tsakanin waɗanda ba Hausawa ba.

- **Ilimi**

  Hulɗa ta kasuwanci tsakanin ƙasashen Larabawa daga Afirka ta arewa da shigowar addinin Musulunci sun yi sanadiyyar zuwan Larabawa da malamai ƙasar Hausa don yaɗa addinin Musulunci. Masu jihadi ƙarƙashin jagoranci Shaihu Usmanu Ɗanfodiyo sun taka muhimmiyar rawa wajen koyar da ilimin addinin Musulunci. Tawagar malamai da suka yi ta zuwa ƙasar Hausa sun zauna a garuruwan Hausa kuma sun koyi harshen Hausa. Haka ma Hausawa sun shiga wasu garuruwan da ƙasashe wajen neman ilimi, zaman Hausawa a wasu garuruwan ya haifar da ƙaruwar masu magana da harshen Hausa.

- **Riƙo da Harshe da Al'adu**

  Wani dalilin da ya haifar da yaɗuwar harshen Hausa a wasu garuruwa da ƙasashen da ba na Hausawa ba shi ne ɗabi'ar Hausawa ta yin riƙo da harshensu da al'adunsu a duk inda suka samu kansu. Wannan ya sa wasu ƙabilun sun riƙi al'adar

Bahaushe da kuma koyan harshen Hausa. Wannan ya ƙara ƙarfin harshen Hausawa a idon duniya. Wannan halin kirki na Bahaushen jiya ya taimaka matuƙa wajen yaɗuwar harshen Hausa a tsakanin wasu ƙabilu na ƙasar nan da ma wasu ƙasashen.

- **Yaƙe-Yaƙe**

Amfani (2012) ya bayyana cewa Bahaushe an san shi da jaruntaka. Wato dai Hausawa mutane ne jarumai kamar yadda tarihin ƙasar Hausa ya nuna. Harshen Hausa ya yaɗu a sakamakon yaƙe-yaƙe da Hausawa suka yi a wasu garuruwan. Misali, da zarar an ci gari da yaƙi sai a naɗa musu shugaba, kuma Hausawa kan zauna a irin wannan gari su ci-gaba da yin amfani da harshen Hausa wajen kasuwanci da bayar da ilimi. Yaƙi yana gurgunta bunƙasar harshe, shi ya sa ƙananan harsuna ba su yi tasiri ba, sai masu magana da Hausa suka ci-gaba da ƙaruwa. Bugu da ƙari, yaƙe-yaƙen da aka yi a tsakanin garuruwan Hausawa ya sanya wasu Hausawan sun fantsama zuwa wasu garuruwa ko ƙasashe inda suka zauna suka ci-gaba da yin amfani da Hausa wanda hakan ya jawo wasu ƙananan ƙabilu yin amfani da Hausa.

- **Yawan Jama'a**

Muhammad (2006: 7) ya bayyana cewa "Yawan jama'a yana ɗaya daga cikin ma'aunan da masana ilimin harshe suke yin amfani da shi wajen gwada matsayin harshe dangane da ci-gabansa a rayuwar kowace al'umma". Ya ƙara da cewa "Kusan duk masana da aka aminta da su, sun yi tarayya kan cewa a nahiyar Afirka ban da Larabci, Hausa ita ta fi yawan zunzurutun masu amfani da ita. Saboda haka, yawan da Hausa take da shi ya yi tasiri wajen yaɗuwar harshen Hausa a Nijeriya da nahiyar Afirka.

Idan ka duba duk dalilan da na kawo maka za ka ga cewa suna da alaƙa da yanayi na Hausawa. Yanzu kuma bari mu waiwayi wasu dalilan da suka taimaka wa waɗanda muka ambata a baya. Waɗannan dalilai su ne:

- **Bunƙasar Tsarin Rubutu da Samar da Littattafai**

Kamar yadda Muhammad (2006: 9) ya bayyana cewa "Daga cikin tarin harsunan Nijeriya ɗari huɗu (400), Hausa duk ta fi girma, kuma tana sahun gaba wajen samun sauran siffofi na rayayyen harshe, ko ma daɗewa da samun rubutun ajami da rubutun boko". A nan ina so na nuna maka cewa waɗannan hanyoyin rubutu sun taka muhimmiyar rawa wajen kawo yaɗuwar harshen Hausa. Domin an yi rubuce-rubuce da dama cikin Hausa ko dai ta hanyar ajami ko kuma boko wanda hakan

ya sa sha'awar koyon harshen ga wasu al'ummomin. Bugu da ƙari, samar da jaridu cikin ajamin Hausa da rubutun boko su ma sun taka rawa, har ma da samar da littattafai na karatu don nishaɗantuwa.

- **Nazarin Hausa a Jami'o'i na Ciki da Wajen Nijeriya**
  Nazarin Hausa a jami'o'i na ciki da wajen Nijeriya ya taimaka matuƙa wajen yaɗuwar harshen Hausa a tsakanin ƙabilu daban-daban. Inda aka fara nazarin Hausa a nan ƙasar ita ce Jami'ar Bayero Kano lokacin da take Kwaleji ƙarƙashin Jami'ar Ahmadu Bello Zariya. Bayan Jami'ar Bayero akwai Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya da ta Usmanu Ɗanfodiyo da ke Sakkwato da ta Maiduguri da sauransu da yawa haɗa da kwalejojin ilimi duk sun taka rawar gani wajen yaɗuwar harshen Hausa. An samu ɗaliban wasu ƙabilun daban-daban da suka nazarci Hausa a matakin digiri kuma suka ci-gaba da koyar da shi a wasu makarantun. Bugu da ƙari, samar da jami'o'i a ƙasashen ƙetare musamman a Turai da Amurka inda ake koyar da Hausa. A Amurka ana koyar da Hausa a jami'o'i da suka haɗa da Jami'ar Indiana da ta Wisconsin da ta Stanford da ta California a Los Angeles da makamantansu. A Turai kuwa akwai jami'o'i da suka ƙunshi Jami'ar London ƙarƙashin Makarantar Binciken Ƙasashen Gabas da Nahiyar Afirka (School of Oriental and African Studies) da ta Leipzig da ta Koln da ta Frankfurt da Hamburg da ta Warsaw da sauransu.

- **Amfani da Hausa a Kafofin Sadarwa na Gida da na Waje**
  Wani dalilin da ya ƙara ƙarfafa yaɗuwar harshen Hausa a ko'ina shi ne amfani da harshen a kafofin sadarwa na rediyo da na talabijin. Ana yin amfani da Hausa a gidajen rediyo da na talabijin a arewacin Nijeriya wannan ya taimaka wajen yaɗuwar Hausa da buƙatar a koyi harshen don jin shirye-shirye da labarai na kafofin sadarwa. Har la yau, ka san cewa ana yin amfani da Hausa a kafofin watsa labarai na ƙetare, kamar gidan rediyon BBC na London da na Muryar Amurka da ke Washington da na Alƙahira a Masar da na Beijing a ƙasar Sin da na Deutsche Welle a Jamus da na Iran da sauransu. Zan waiwaye su nan gaba don ka kara fahimtar su da kyau.

  Har yanzu idan ka sake dubawa za ka ga zamani yana zuwa da wasu tsare-tsare da su ma suke ƙarfafa yaɗuwar harshen Hausa a ciki da wajen Nijeriya. Misali, shirin duniya a tafin hannu ko gama duniya da kafofin sadarwa na zamani (irin su *WhatsApp* da *Facebook* da *Twitter* da *Instagram* da makamantansu). Wasu masana na ganin cewa harshen Hausa harshe ne mai yaɗo a kan kansa da kuma karɓuwa a idon duniya. Harshen Hausa ya

kasance ɗaya daga cikin manyan harsuna na duniya saboda yawan jama’ar da suke amfani da shi. Duk bayanan da ka ji tun daga kashi na ɗaya zuwa na wannan (wato na huɗu) duk shimfiɗa nake yi maka dangane da kwas ɗin hanyar sadarwar a harshen Hausa.

**Auna Fahimta na 1**

Kawo sunayen Jami'o'in da nazarin Hausa na ciki da wajen Nijeriya guda uku-uku. Jami'ar Bayero akwai Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya da ta Usmanu Ɗanfodiyo

Yi cikakken bayani tare da misalai kan biyu daga cikin dalilan da suka haifar

Da yaɗuwar Hausa a wajen ƙasar Hausa?

## 4.4 Taƙaitawa

A wannan kashi ka fahimci cewa:

- Yaɗuwar harshen Hausa yana da alaƙa da tarihi da ɗabi'ar Hausawa.
- Girman harshen Hausa da kasuwanci / fatauci da riƙo da al'ada da harshe da yaƙe-yaƙe da ilimi da yawan Hausawa sun ƙarfafa ƙaruwar masu magana da harshen Hausa.
- Dalilai kamar bunƙasar hanyar rubutun Hausa cikin ajami da boko da nazarin Hausa a mataki na jami'a da kwalejin ilimi da amfani da Hausa a kafofin sadarwa na ciki da wajen Nijeriya da kafofin sadarwa na zamani sun ƙara ƙarfafa yaɗuwar masu magana da Hausa a ko'ina.

## 4.5 Ma'anar Muhimman Kalmomi

- Fatauci – shi ne sayan kaya daga wani wuri akai wani wuri
- Ƙaura – tafi ko tashi daga wani wuri zuwa wani wuri

## 4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Abubakar, A. (2006). Matsayin Nazarin Harshen Hausa a Yau. *Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies*. No. 4 Vol. 4.

Adamu, M. (1978). *The Hausa Factor in West African History*. London: Odford Uniɓersity Press.

Adamu, M. T. (1997). *Asalin Hausawa da Harshensu*. Kano: Ɗansarkin Kura Publishers.

Alhassan, H. da Wasu. (1988). *Zaman Hausawa*. Lagos: Islamic Publication Bureau.

Amfani, A. H. (2012). Hausa Da Hausawa: Jiya Da Yau Da Gobe. In Amfani, H.A, et al (eds.) *Champion of Hausa Cikin Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press.

Sani, M. A. Z. (2009). *Siffofin Daidaitacciyar Hausa*. Kano: Benchmark Publishers Limited.

Tudun Wazirchi, A. G. I. (2009). *Mu San Kare-Karenmu*. Kano: Rurum Printing and Publishing Company.

Muhammad, Ɗ. (2006). Tsakanin Hamada da Hamdala: Waiwayen Gudunmawar Jami'o'i da Haɓaka Harshen Hausa. *Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies*. No. 4 Ɓol. 1.

Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa a Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Zaria: NNPC.

Zarruƙ, R. da Wasu. (1986). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa*. Ibadan: University Press Limited.

## 4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**Amsoshin Auna Fahimta na 1**

1. Kawo sunayen Jami'o'in da nazarin Hausa na ciki da wajen Nijeriya guda uku-uku.

Na cikin Nijeriya

i- Jami'ar Bayero ta Kano
ii- Jami'ar Ahmadu Bello ta Zariya
iii- Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo ta Sakkwato

Na wajen Nijeriya

i- Jami'ar Indiana
ii- Jami'ar Wisconsin
iii- Jami'ar Stanford

2. Yi cikakken bayani tare da misalai kan biyu daga cikin dalilan da suka haifar
3. Da yaɗuwar Hausa a wajen ƙasar Hausa?

- **Yawan Jama'a**

Muhammad (2006: 7) ya bayyana cewa "Yawan jama'a yana ɗaya daga cikin ma'aunan da masana ilimin harshe suke yin amfani da shi wajen gwada matsayin harshe dangane da ci-gabansa a rayuwar kowace al'umma". Ya ƙara da cewa "Kusan duk masana da aka aminta da su, sun yi tarayya kan cewa a nahiyar Afirka ban da Larabci, Hausa ita ta fi yawan zunzurutun masu amfani da ita. Saboda haka, yawan da Hausa take da shi ya yi tasiri wajen yaɗuwar harshen Hausa a Nijeriya da nahiyar Afirka.

Idan ka duba duk dalilan da na kawo maka za ka ga cewa suna da alaƙa da yanayi na Hausawa. Yanzu kuma bari mu waiwayi wasu dalilan da suka taimaka wa waɗanda muka ambata a baya. Waɗannan dalilai su ne:

- **Bunƙasar Tsarin Rubutu da Samar da Littattafai**

Kamar yadda Muhammad (2006: 9) ya bayyana cewa "Daga cikin tarin harsunan Nijeriya ɗari huɗu (400), Hausa duk ta fi girma, kuma tana sahun gaba wajen samun sauran siffofi na rayayyen harshe, ko ma daɗewa da samun rubutun ajami da rubutun boko". A nan ina so na nuna maka cewa waɗannan hanyoyin rubutu sun taka muhimmiyar rawa wajen kawo yaɗuwar harshen Hausa. Domin an yi rubuce-rubuce da dama cikin Hausa ko dai ta hanyar ajami ko kuma boko wanda hakan ya sa sha'awar koyon harshen ga wasu al'ummomin. Bugu da ƙari, samar da jaridu cikin ajamin Hausa da rubutun boko su ma sun taka rawa, har ma da samar da littattafai na karatu don nishaɗantuwa.

# RUKUNI NA BIYU (2) HANYOYIN SADARWAR HAUSA TA GARGAJIYA I

Kashi Na 1 Ma’anar sadarwa da irenta
Kashi Na 2 Sadarwa ta zane-zane
Kashi Na 3 Sadarwa ta kayan kiɗa
Kashi Na 4 Sadarwa ta amfani da sauti

## Kashi Na Ɗaya Ma’anar Sadarwa Da Ire-Irenta

### Abubuwan da Suke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Ma’anar sadarwa
1.4 Ire-iren sadarwa
  1.4.1 Hanyar sadarwa ta Gargajiya
  1.4.2 Hanyar sadarwa ta zamani
  Auna Fahimta
1.5 Taƙaitawa
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amsoshin Auna Fahinta

### 1.1 Gabatarwa

Kamar yadda muka gani a darussa huɗu da suka gabata, mun ga asalin harshen Hausa da Hausawa da kuma irin yadda harshen Hausa ya bunƙasa ta hanyoyi da dama tun daga tsarin zamantakewarsa da wasu baƙi na kusa da na nesa da ƙaurace-ƙaurace da neman ilimin har zuwa lokacin da harshen Hausa ya sami hanyar yin rubutu da kuma yadda ake nazartar harshen a wasu Kwalejoji da Jami’o’i na cikin gida da na waje. Amma a wannan rukunin za mu karkatar da akalar wannan bayani zuwa ɓangaren hanyoyin sadarwar Hausawa ta gargajiya da ta zamani. Shi kuwa wannan kashi zai fuskanci ma’anar sadarwa da ire-irenta.

### 1.2 Manufa

A ƙarshen wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Bayyana ma’anar sadarwa.
- Kawo hanyoyin sadarwar Hausawa na gargajiya
- Kawo hanyoyin sadarwar Hausawa na zamani

## 1.3 Ma’anar Sadarwa

Kamar yadda masana suka yi bayani kan kalmar sadarwa, wasu sun bayyana kalma da cewa “sadarwar hanya ce ta tura wa ko karɓar saƙonni daga wajen wani mutum ko mutane ta hanyar amfani da wasu hanyoyi daban- daban don isar da saƙonni a gare su. Haka ma, Zarruƙ R.M (2011), ya bayyana sadarwa da cewa “sadarwa ita ce isar da saƙo tsakanin ɓangarori biyu: Mai bayar da saƙo da kuma mai karɓar saƙo ta hanyar kafar isar da saƙo wacce ka iya zama mutum ko waninsa, sannan kuma cikin sigar da dukkan ɓangarorin da abin ya shafa za su iya fahimta.”

Bugu da ƙari, za mu iya cewa sadarwa wata hanya ce ta hanyar isar da da wani tunani ko saƙo ko bayani daga wani zuwa wani ko da wani zuwa wasu.

### 1.3.1 Ire-iren Hanyoyin sadarwa na Hausa

Dukkan al’ummun duniya, suna da hanyoyin da suke amfani da su wajen isar da saƙonnin a tsakaninsu. Daga cikin ire-iren waɗannan hanyoyi akwai hanyar sadarwa da gargajiya da kuma ta zamani.

#### 1.3.1.1 Hanyoyin sadarwa na gargajiaya

Wannan hanyar sadarwa ta gargajiya tana ɗaya daga cikin tsohuwar hanyar isar da saƙon Bahauhse ce wadda suke amfani da ita tum kafin zuwan Larabawa da Turawa. Daga cikin irin waɗannan hanyoyi akwai:

i- Hanyar sadarwa ta baka-da-baka
ii- Hanyar amfani da alamu ko zane
iii- Hanyar amfani da gaɓɓoɓi na jiki.
iv- Hnayar amfani da kayan kiɗa
v- Saƙon kar-ta-kwana

#### 1.3.1.2 Hanyoyin sadarwa na gargajiaya

An bayyana wannan hanyar sadarwa ta zamani da cewa hanya ce da ake isar da saƙo ta hanyar amfani da wata na’ura ko sakamakon samun cigaba da aka samu na Zamani. Wannan hanya ce da mutum ɗaya kan isar da saƙo ga ɗimbun al’umma. Na’urorin da ake amfani da su wajen isar da saƙo ta wannan hanya sun haɗa da:

i- Rediyo
ii- Talabijin
iii- Na ura me kwakwalwa
iv- wayar tafi da gidanka
v- Jarida da sauransu.

**Auna Fahimta na 1**

1- Me ake nufi da kalmar sadarwa?

2- Yi taƙaitaccen bayani kan hanyar sadarwa ta zamani tare da misalan na’urori guda huɗu.

## 1. 4 Taƙaitawa

A wannan darasi an koyi abubuwa kamar haka:

1. Ma'anar sadarwa
2. Ire-iren sadarwa a Hausa
3. Abubuwan da ake amfani da su wajen isar saƙo na gargajiya da na zamani

## 1.5 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 1.6 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

**Amsoshin Auna Fahimta na 1**

1. Me ake nufi da kalmar sadarwa?

i- sadarwar hanya ce ta tura wa ko karɓar saƙonni daga wajen wani mutum ko mutane ta hanyar amfani da wasu hanyoyi daban-daban don isar da saƙonni a gare su. Haka ma,

ii- Zarruƙ R.M (2011), ya bayyana sadarwa da cewa "sadarwa ita ce isar da saƙo tsakanin ɓangarori biyu: Mai bayar da saƙo da kuma mai karɓar saƙo ta hanyar kafar isar da saƙo wacce ka iya zama mutum ko waninsa, sannan kuma cikin sigar da dukkan ɓangarorin da abin ya shafa za su iya fahimta."

iii- Sadarwa wata hanya ce ta hanyar isar da da wani tunani ko saƙo ko bayani daga wani zuwa wani ko da wani zuwa wasu..

2. Yi taƙaitaccen bayani kan hanyar sadarwa ta zamani tare da misalan na'urori guda

i- Rediyo

ii- Talabijin

iii- Na ura me kwakwalwa

iɓ- wayar tafi da gidanka

ɓ- Jarida da sauransu

# Kashi Na Biyu (2) Hanyar Sadrawa Ta Zane-Zane Ko Alama

## Abubuwan Da Suke Ciki


2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Hanyar sadarwa zane-zane
  2.3.1 Zanen suna
  2.3.2 Zanen fuska
  2.3.3 Alamar Feƙe da Sassaƙa
  Auna Fahimta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma'anar wasu kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Auna Fahinta


## 2.1 Gabatarwa

Kamar yadda muka gani a darussa biyun da suka gabata, mun ga abun da ake nufi da sadarwa ta gargajiya da zamani da kuma yadda ake aiwatar da su. Bayan haka, mun ga ire-iren na'urorin da ake amfani da su wajen aiwatar da sadarwa ta zamani, amma a wannan darasin za mu yi bayani kan hanyar sadarwa ta zane-zane.

## 2.2 Manufa

A ƙarshen wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Bayyana zane-zane
- Kawo ire-iren zane-zane da Hausawa suke amfani da shi wajen isar da saƙo
- Sanin hikimomin da zane-zane suke da su

## 2.3 Zane-zane

Zane-zane wata alama ce da ake amfani da ita wajen isar da saƙo. Zaruƙ (2011), ya ce, a gargajiyance, a zamanin baya, fatake suna da alamomin da suka keɓanta da kowane daga cikinsu, da suke zanawa a jikin dabbobinsu. Idan masu korar dabbobi suka kora aka kai kasuwa, koda mai kayan bai je kasuwa ba, to za a ware nasa a bai wa dillalinsa ya sayar masa. Haka nan kuma koda a zaman gida, idan dabbar wani ta

shiga cikin ayarin wasu dabbobin a wajen kiwo har ta kai ga ta shiga gidan wani, da zarar magariba ta ƙarato, to idan aka ga wannan baƙuwar dabba, abin yi kawai shi ne za a duba zanen jikinta, da zarar an ga zanen, to an san gidan da ta fito, sai a bai wa yaro ya ja ya kai gidan masu ita.

### 3.3.1 Zanen Suna

Tun kafin kowane baƙo ya zo ƙasar Hausa, Bahaushe yana da hanya da yake bi wajen raɗa wa jariri ko jaririya suna. Ana samun siyaye; wato karan rama, a ɓara shi ko a tsaga shi gida biyu, sai a samu guda bakwai a zazzana alamomi daban-daban a jiki, sai a kai wa mai jego ta zaɓi guda a ranar suna. Dukkan wanda ta zaɓa a ciki, sai a dawo da shi zuwa ga dattawan da tun asali su suka zana waɗannan alamomi, da sun ga wanda mai jegon ta zaɓa, to sai su yi amfani da alamar da ke jikin wannan siyaye da mai jego ta zaɓa su ambata sunan abin haihuwa.

Dan gane da wannan magana, ga wani abu da zan ce da ku wanda na jiyo daga Farfesa Bunza (2002), domin guiwarku ta yi ƙarfi, "Ganin haka, masana Hausa ke ganin dole, akwai hanyar sadarwar rubuce a Hausa ta gargajiya".

### 2.3.2 Zanen Fuska

Zanen fuska, tsohuwar al'ada ce ta sadarwar Bahaushe. Ta wannan hanya Bahaushe yake faɗin irin yankin da ya fito da kuma irin sana'ar gidansu a Ƙasar Hausa.

Misali, akwai zanen fuska da ya yi fice da sunan 'Yar Katsina a Ƙasar Hausa. Sannan kuma akwai wani na'u'in bille (zanen fuska ne) da ake yi a ɓarin dama na fuskar mutum wanda mahauta suka keɓanta da shi a Ƙasar Hausa. Idan da za ka ga mutum da 'Yar Katsina a fuskarsa, kuma ga bille a ɓarin dama na fuskarsa, to wannan mutum yana gaya maka cewa, ni mutumin ƙasar Katsina ne kuma sana'ar gidanmu ita ce fawa. Ko kuma kai tsaye yana cewa da kai, ni mutumin Katsina ne kuma mahauci ba tare da ka ji furuci daga bakinsa ba.

### 2.3.3 Alamar Feƙe da Sassaƙa

Waɗannan sana'o'i ne na gargajiyar Bahaushe, waɗanda suke cike da hikima da dabarar isar da saƙo. Waɗannan masu sana'a suna yin zane-zane ne a jikin kayan amfanin gida da sauransu. Suna zana alamomi a jikin akushi, ludayi, butar duma, mafici, ƙwarya da sauransu. Ta irin wannan hanya suke bambanta ludayi, ƙoƙon-sha da kuma butar mai gida. Duk wanda ya ga wannan alama a jikin waɗannan abubuwa da aka lissafa, to ya san cewa wannan buta, ludayi ko ƙoƙo na mai gida ne,

saboda haka ba zai yi wasa da shi ba. Kuma haka abin yake a fannin saƙar tabarma, mafici, malafa, da sauransu.

Idan muka waiwaici Farfesa Bunza (2006), kan wannan magana, za mu ji shi yana cewa: “Daga cikin sana’o’in akwai basira da hikima da suka nuna akwai dabarar sadarwa ta gargajiya a ciki”.

**Auna Fahimta na 1**

1. Zanen fuska yana bayyana yankin da mutum ya fito da kuma irin ______ gidansu
   a Ƙasar Hausa. sana’ar
2. Yi bayani kan sadarwa ta alamar Feƙe da Sassaƙa

## 2.4 Taƙaitawa

A wannan darasi, an koyi abubuwa kamar haka:

- Bayanai kan zane-zane
- Bayani kan zanen suna
- Tsokaci kan zanen fuska
- Kawo bayani kan alamar feƙe ko sassaƙe

## 2.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi

- Feƙe – sana’a ce wadda suke amfani wuƙa ko wasu abubuwa masu kaifi wajen sassaƙe itace.
- Sassaƙa - sana’a ce wadda suke amfani wuƙa ko wasu abubuwa masu kaifi wajen sassaƙa turmi ko ƙoƙiya ta hanyar sarrafa itace.

## 2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 2.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1- Zanen fuska yana bayyana yankin da mutum ya fito da kuma irin ______ gidansu a Ƙasar Hausa.

- sana'ar

2. Yi bayani kan sadarwa ta sana'ar Feƙe da Sassaƙa

   Waɗannan sana'o'i ne na gargajiyar Bahaushe, waɗanda suke cike da hikima da dabarar isar da saƙo. Waɗannan masu sana'a suna yin zane-zane ne a jikin kayan amfanin gida da sauransu. Suna zana alamomi a jikin akushi, ludayi, butar duma, mafici, ƙwarya da sauransu. Ta irin wannan hanya suke bambanta ludayi, ƙoƙon-sha da kuma butar mai gida. Duk wanda ya ga wannan alama a jikin waɗannan abubuwa da aka lissafa, to ya san cewa wannan buta, ludayi ko ƙoƙo na mai gida ne, saboda haka ba zai yi wasa da shi ba. Kuma haka abin yake a fannin saƙar tabarma, mafici, malafa, da sauransu

# Kashi Na Uku (3) Hanyar Sadarwa Ta Kayan Kiɗa Da Busa Da Bugawa

## Abubuwan Da Suke Ciki

3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Kayan kiɗa da busa da bugawa
3.3.1 Ganga
3.3.2 Ƙaho
3.3.3 Rarrabewa ta zaman daidaito
Auna Fahimta
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma'anar wasu kalmomi
3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.7 Amsoshin Auna Fahinta

## 3.1 Gabatarwa

A wannan darasi, za a mayar da hankali kan gabatar wa ɗalibai hanyar sadarwa ta kayan kiɗa. Bugu da ƙari, za kuma a fito da wasu daga cikin nau'o'in kayan kiɗa kamar A wannan ɓangare na kayan kiɗan Bahaushe akwai babbar ganga, banga, ba'ala, badujala, bandiri, bango, duman girke, dundunfa, gangi, jauje, kalangu, kanzagi, kanjau, kotso, kuntukuru, kurya, talle, tandu, tambari, taushi, turu da sauransu.

## 3.2 Manufar Darasi

A ƙarshen wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Bayyana ma'anar kayan kiɗa.
- Ire-iren kayan kiɗa
- Abubuwan da ake la'akari da su a wajen sadarwa

## 3.3 Kayan kiɗa

Kayan kiɗa wasu kayayyaki ne da ake amfani da su wajen samar da wani sauti da kan iya sa nishaɗi tare da isar da wani saƙo daga mai bugawa zuwa ga mai sauraro. Bahaushe yana amfani da kayan kiɗa na gargajiya wajen isar da saƙonni.

### 3.3.1 Ganga

Ganga na ɗaya daga cikin kayayyakin kiɗa. Akwai nau'o'in ganga waɗanda Hausawa suke amfani da su wajen isar da saƙo, ga wasu kamar haka: babbar ganga, banga, ba'ala, badujala, bandiri, bango, duman girke, dundunfa, gangi, jauje, kalangu, kanzagi, kanjau, kotso, kuntukuru, kurya, talle, tandu, tambari, taushi, turu. Ana kaɗa ganga domin sanar da yin wasanni kamar irin su kokawa da saurnsu. Misali, idan za a yi wasan kokawa, to mai ganga yakan yi ta kaɗawa na tsawon lokaci domin sanar da mutane cewa, an fara taruwa. Wannan ita za ta saka mutane su yi ta fitowa zuwa gurin da suke jin wannan amon (Zarruƙ da Wasu, 2011)

### 3.3.2 Ƙaho

Ƙaho na ɗaya daga cikin kayayyakin da ake busa. Akwai nau'o'in ƙaho dama, kamar ƙaho na akuya da na rago da na barewa da sa ko saniya da sauransu. Ana busa ƙaho domin sanar da mazaje su yi shirin fita daji domin farauta.

### 3.3.3 Sarewa

Samari kan busa wa 'yan matansu sarewa domin sanar da su cewa su fito zance.

### 3.3.4 Kurya

Kurya ganga ce da ake kaɗa ta a lokacin da ake son sanar da jama'ar gari cewa su yi shirin fita yaƙi a lokacin yaƙe-yaƙe.

### 3.3.5 Kuge

Wasu ƙarafuna ne na kiɗa da ake buga su da juna. Ana amfani da su wajen sanar da mazaje fita yaƙi.

### 3.3.6 Bindiga

Ana harba bindiga domin sanar da jama'a ganin watan azumi ko na sallah. Sannan kuma idan aka idar da sallar Juma'a a babban masallaci akan harba bindiga domin sanar da matan da ke cikin gida cewa an sauko daga Juma'a domin suma su shirya su yi sallar azahar.

**Auna Fahimta na 1**

1. Me ya sa ake amfani da ƙaho wajen sadarwa?
2. Kawo ire-iren ganga guda biyar.

## 3.4 Taƙaitawa

A wannan darasi, an koyi abubuwa kamar haka:

- Ma’anar kiɗa da busa da kuma bugawa
- Ire-iren ganga
- Misalan kayan kiɗa da busawa da bugawa
- Bambanci tsakanin kayan kiɗa da busawa da bugawa.

## 3.5 Ma’anar Muhimman Kalmomi

- Kurya: - ganga ce da ake kaɗa ta a lokacin da ake son sanar da jama’ar gari cewa su yi shirin fita yaƙi a lokacin yaƙe-yaƙe.
- Kuge - wasu ƙarafuna ne na kiɗa da ake buga su da juna. Ana amfani da su wajen sanar da mazaje fita yaƙi.

## 3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Me ya sa ake amfani da ƙaho wajen sadarwa?
- Ana busa ƙaho domin sanar da mazaje su yi shirin fita daji domin farauta.
2. Kawo ire-iren ganga guda biyar.

i- banga
ii- ba’ala
iii- badujala
iɓ- bandari
ɓ- bango
ɓi- duman da sauransu.

girke, dundunfa, gangi, jauje, kalangu, kanzagi, kanjau,
kotso, kuntukuru, kurya, talle, tandu, tambari, taushi, turu

# Kashi Na Huɗu (4) Sadarwa Ta Amfani Da Sauti

## Abubuwan Da Suke Ciki

4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Sauti
4.4 Ire-Iren Sauti sadarwa
4.4.1 Shela/Yekuwa
4.4.2 Guɗa
4.4.3 Ihu
4.4.4 Kururuwa
4.4.5 Kuka
4.4.6 Sowa
Auna Fahinta
4.5 Taƙaitawa
4.6 Ma'anar wasu kalmomi
4.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.8 Amsoshin Auna Fahimta

## 4.1 Gabatarwa

Wannan kashi ya kawo ma'ana da bayanin sadarwa ta hanyar sauti ko amo. An kawo ire-iren sadarwar da ake ta amfani da wasu ɓangarori na jiki kamar ido ko baki ko hanci a samar da wani amo domin isar da saƙo.

## 4.2 Manufar Darasi

A ƙarshen wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Kawo ma'anar sauti
- Sanin ire-iren sassan da ake samar da sauti
- Bayyana sautukan da ake isar da saƙo

## 4.3 Sauti

Sauti na nufin wata ƙara da ke samuwa a sanadiyar amfani da wani sashi na baki ko hanci ko ido ko hannu da hanci. Haka ma, za a iya samun ƙara a sanadiyar haɗuwar wani abu da wani kamar ƙarfe da ƙarfe ko kwalɓa da kwalɓa ko hannu da hanci da sauransu. Bahaushe yana

amfani da sauti wajen sadarwa. Sauti kuwa a nan yana nufin amo wanda ka iya zama na murya ko waninta (Zarruƙ da Wasu 2011).

## 4.4 Ire-iren sautuka

Ta fuskar sautukan da ake amfani da su wajen isar da saƙo, akwai shela/yekuwa da guɗa da ihu da sauransu.

### 4.4.1 Shela/Yekuwa

A gargajiyance, shela/yekuwa, hanya ce ta isar da saƙo daga mai gari/sarki zuwa ga talakawa. Ta wannan hanya ake sanar da jama'a wani saƙo da sarki yake son su sani. Shugaban maroƙa; wato sanƙira kenan, shi yake yin shela. Yakan ce, "Yeeeeekuwa jama'ar gari, sarki ya gaishe ku, ya kuma ya gaishe ku, ya ce a sanar da ku cewa, gobe idan Allah ya kai mu, akwai noman gandun sarki".

### 4.4.2 Guɗa

Ƙara ce mai ƙarfi da ake fitar da ita ta hanyar baki da hanci. Mata ne suke yin guɗa domin sanar da haihuwa ko kuma wani abin farin ciki da ya faru a gida. Ana yin guɗa ta hanyar matse hanci a rufe shi da yatsu sannan a lanƙwasa harshe ana karkaɗa shi sai kuma a turo iska daga maƙogwaro.

### 4.4.3 Ihu

Ihu alama ce da Bahaushe ke amfani da ita wajen nuna shiga halin damuwa tare kuma da neman agaji. Haka nan kuma idan ana aikin gayya ko a gida ko a gona, akan kwarma ihu.

### 4.4.4 Kururuwa

Kururuwa ihu ne na mutane masu yawa a lokaci guda. Ana yin kururuwa domin neman agajin gaugawa a lokacin da aka tashi ɓarawo ko kuma a halin gobara.

### 4.4.5 Kuka

Kuka hanya ce ta sanar da ɓacin rai ko shiga wani mummunan hali ko wata damuwa da tafi ƙarfin juriyar mutum.

### 4.4.6 Sowa

Sowa ita ce kuka haɗe da ihu; wato mutum yana kuka da ƙarfi. Alama ce ta nuna matsanànciyar damuwa ko tashin hankali.

**Auna Fahimta**

1. Mene ne sauti?
2. Kawo ire-iren sadarwa ta amfani da sauti guda biyar.

## 4.5 Taƙaitawa

A wannan darasi, an koyi abubuwa kamar haka:

- Ma’anar sauti na sadarwa
- Ire-iren sautukan sadarwa
- Misalan sautukan sadarwa
- Bambanci tsakanin sautukan sadarwa.

## 4.6 Ma’anar Muhimman Kalmomi

- Kururuwa: - ihu ne na mutane masu yawa a lokaci guda
- Sowa: - ita ce kuka haɗe da ihu

## 4.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 4.8 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Mene ne sauti?

   Sauti na nufin wata ƙara da ke samuwa a sanadiyar amfani da wani sashi na baki ko hanci ko ido ko hannu da hanci. Haka ma, za a iya samun ƙara a sanadiyar haɗuwar wani abu da wani kamar ƙarfe da ƙarfe ko kwalɓa da kwalɓa ko hannu da hanci da sauransu. Bahaushe yana amfani da sauti wajen sadarwa. Sauti kuwa a nan yana nufin amo wanda ka iya zama na murya ko waninta.

2. Kawo ire-iren sadarwa ta amfani da sauti guda biyar.

**i-** shela/yekuwa
ii- kuka
iii- sowa
iɓ- kururuwa
ɓ - guɗa
ɓi- ihu

## RUKUNI NA UKU SADARWA GARGAJIYA TA SASSAN JIKI

Kashi Na 1 Sadarwa ta kai
Kashi Na 2 Sadarwa ta baki
Kashi Na 3 Sadarwa ta hannu
Kashi Na 4 Sadarwa ta ido

## KASHI NA ƊAYA (1) SADARWA TA SASSAN JIKI

### Abubuwan da Suke Ciki

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Sadarwa ta amfani da kai
    1.3.1 Girgiza Kai
    13.2 Ɗaga Kai Sama
    1.3.3 Girgiza Kai Dama da Hagu
    1.3.4 Sunkuyar da kai
    Auna Fahimta
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma'anar wasu kalmomi
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amsoshin Auna Fahinta



### 1.1 Gabatarwa

A wannan kashi an yi bayani kan yadda ake aiwatar da sadarwa ta hanyar amfani da kai. Sannan an kawo ire-irensa sadarwa da ake amfani da kai wajen gudanar da ita. Amma yana da kyau mu fahimci cewa, shi ma kai yana ɗaya daga cikin abubuwan da ake amfani da shi wajen isar da saƙo. Sannan an kawo bayanai kan sadarwa ta amfani da kai.



### 1.2 Manufar Darasi

Bayan kammala wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:
- Bayani a kan sadarwa kai.
- Bayyana ire-iren sadarwa da ake yi da kai.
- Bambance nau'o'in sadarwa ta kai

## 1.3 Sadarwa ta amfani da kai

Ana amfani da kai a wajen isar da saƙo ta hanyar yin ishara a tsakanin al’ummar Hausawa domin taƙaita magana da fatar baki. Daga isharorin da ake yi da kai akwai; girgiza kai da ɗaga kai sama da girgiza kai dama da hagu da sunkuyar da kai.

### 1.3.1 Girgiza Kai

Wannan hanya ce da ake sadarwa a lokacin da wani abu ya ba mutum mamaki ko ya burge shi ko ya ƙayatar. Kuma ana yi haka ne ta hanyar maimaita ɗaga kai sama da ƙasa.

### 13.2 Ɗaga Kai Sama

Ana yin wannan sadarwa ne ta hanyar ɗaga kai wajen baya sau ɗaya. Wannan sadarwa ce da take nufin mutum ya amince ko ya yarda da wani abu da a ka yi ko aka faɗa masa.

### 1.3.3 Girgiza Kai Dama da Hagu

Wannan sadarwa ce da ake yi ta hanyar mutum ya girgiza kansa ta gefen dama da na hagu. Hakan yana nufin mutum bai amince da wani abu da aka faɗa masa ko ya ji.

### 1.3.4 Sunkuyar da kai

Wannan sadarwa ce da ake yi ta hanyar da mutum za sunkuyar da kansa ƙasa. Hakan na nuna cewa mutum ya ji kunya dangane abun da ya yi ko wani abu da aka faɗa masa wanda kan haifar da jin kunya.

**Auna Fahimta**

1. Shin ana amfani da kai wajen sadarwa?
2. Yi bayani biyu daga cikin hanyoyin sadarwa na kai

## 1.4 Taƙaitawa

A wannan darasin an koyi abubuwa kamar haka:

i. Ma'anar sadarwa ta kai
ii. Ire-iren sadarwa ta kai.

## 1.5 Ma’anar Wasu Kalmomi

Sukuyar da kai – tura kai gaba fuska ta kalli ƙasa
Girgiza kai – kaɗa kai daga dama zuwa hagu

## 1.5 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

CNHN, (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami’ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity press.

Lawal, N. da Adamu, H.B. (2020). Saayee A Wasu Sassan Jiki a Al’adun Hausawa. In *Ɗaunɗaya Journal of Hausa Studies*, Ɓol.2 (3). Sokoto: Department Of Nigerian Languagaes, Usmanu Ɗanfodiyo Uniɓersity.

Sallau, B.A. (2010). *Wanzanci da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kaduna: M.A. Najiu Professioinal Printers.

Sallau, B.A. (2013). *Wanzanci da Sauye-Sauyen Zamani*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press Limited.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 1.7 Amsoshin Tamabayoyin Auna Fahimta

1. Shin ana amfani da kai wajen sadarwa?
   Gaskiya ne
2. Yi bayani biyu daga cikin hanyoyin sadarwa na kai

- Girgiza Kai
  Wannan hanya ce da ake sadarwa a lokacin da wani abu ya ba mutum mamaki ko ya burge shi ko ya ƙayatar. Kuma ana yi haka ne ta hanyar maimaita ɗaga kai sama da ƙasa.
- Ɗaga Kai Sama
  Ana yin wannan sadarwa ne ta hanyar ɗaga kai wajen baya sau ɗaya. Wannan sadarwa ce da take nufin mutum ya amince ko ya yarda da wani abu da a ka yi ko aka faɗa masa.
- Girgiza Kai Dama da Hagu
  Wannan sadarwa ce da ake yi ta hanyar mutum ya girgiza kansa ta gefen dama da na hagu. Hakan yana nufin mutum bai amince da wani abu da aka faɗa masa ko ya ji.
- Sunkuyar da kai
  Wannan sadarwa ce da ake yi ta hanyar da mutum za sunkuyar da kansa ƙasa. Hakan na nuna cewa mutum ya ji kunya dangane abun da ya yi ko wani abu da aka faɗa masa wanda kan haifar da jin kunya.

## Kashi Na Biyu (2) Sadarwa Ta Baki

### Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Sadarwa ta baki
 2.3.1 Murguɗa Baki
 2.3.2 Zumɓura Baki
 2.3.3 Buɗe Baki
 2.3.4 Gwalo
 2.4.5 Zunɗe
 2.4.6 Murmushi
 Auna fahinta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma’anar wasu kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Auna Fahinta

### 2.1 Gabatarwa

A wannan kashi an bayyana ma'anar sadarwa ta baki. Baki na ɗaya daga cikin sassa na fuska wanda ake amfani da shi wajen isar da wasu saƙonni. Amma a wannan kashi ya kamata mu fahimci cewa, shi ma baki yana bada gudummawa wajen sadarwa. An kawo ire-iren sadarwar ta baki tare da misalai.

### 2.2 Manufar Darasi

Bayan kammala wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Bayani a kan sadarwa baki.
- Bayyana ire-iren sadarwa ta baki.
- Bambance nau’o’in sadarwa na baki

### 2.3 Baki

Baki yana ɗaya daga cikin sassa na fuska wanda ake amfani da shi wajen isar da wani saƙo. Akwai sadarwa da dama da ake aiwatar da baki. Irin wannan sadarwa ta haɗa da:

- Murguɗa Baki
- Zumɓura Baki

- Buɗe Baki
- Gwalo

### 2.3.1 Murguɗa Baki

Hanya ce da ake motsa leɓen ƙasa da na sama a lokaci guda. Saƙon da ake isarwa a irin wannan hanyar sadarwa ta ƙunshi rashin kunya ko raina wani ko wata.

### 2.3.2 Zumɓura Baki

Wannan hanya ce wadda ake turo leɓɓa (na sama da na ƙasa) gaba domin isar da wani saƙo. Idan yaro ya zumɓura baki, wannan na nuna shagwaɓa, idan kuma babban mutum ne ya zumɓuri baki, to wannan na nufin raini ne.

### 2.3.3 Buɗe Baki

Wannan hanya ce wadda ake buɗe baki ma'ana a raba leɓe sama da ƙasa domin isar da wani saƙo. Idan mutum ya buɗe baki, wannan na sadarwa ta mamaki, idan kuma babban mutum ya buɗe baki, to wannan na nufin mamaki**.**

### 2.3.4 Gwalo

Ana yin gwalo ne ta hanyar gwale idanu tare da zaro harshe waje a kalli wanda ake yi wa. Akan yi gwalo ne domin muzantawa. Yawanci an fi yi wa wanda aka raina. Haka kuma isharar gwalo ta fi faruwa a tsakanin abokai ko kuma yara su yi wa babban gwalo.

### 2.4.5 Zunɗe

Irin wannan sadarwa ta baki ana yin ta hanyar kaikaitar idon wanda za a yi wa zunɗen ne sai a kuma kalli wanda za a ba shi labarin sai masu yin zunɗen su tura bakunansu gaba ana yi ana dawowa da shi gaba da baya ana nuna wanda ake zunɗe ana ɗan gantsarewa. Wannan irin sadarwa babu abin da da take nunawa sai munafunci da haɗa kisisinar tsiya wanda in ba a yi sa'a ba wanda ake yi wa ya gane sai rikici ya tashi. Haka kuma, mai yin zunɗe ana nuna cewar lallai mutum matsoraci ne tun da ba za ya iya fitowa ya faɗi abin da ake so game da wanda yake zunɗen ba (Adamu, 1995:26).

### 2.4.6 Murmushi

Sadarwa ce da ake yi domin nuna farin-ciki ko soyayya ko murna ko amincewa da juna. Ana yin wannan ishara ce ta hanyar mutum zai saki fuskarsa tare da da ɗan ɓuɗe bakinsa yadda zai fito da haƙoransa waje.

**Auna Fahimta**

| |
|---|
| 1 Shin ana amfani da kai wajen sadarwa? |
| 2. Yi bayani biyu daga cikin hanyoyin sadarwa na kai |

## 2.5 Taƙaitawa

A wannan darasin an koyi abubuwa kamar haka:

i. Ma'anar sadarwa ta baki
ii. Ire-iren sadarwa ta baki.

## 2.6 Ma'anar Wasu Kalmomi

Gwalo: - shi ne gwale idanu tare da zaro harshe waje a kalli wanda ake yi wa. Zumɓuro baki- turo leɓɓa gaba

## 2.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

CNHN, (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity press.

Lawal, N. da Adamu, H.B. (2020). Saayee A Wasu Sassan Jiki a Al'adun Hausawa. In *Ɗaunɗaya Journal of Hausa Studies,* Ɓol.2 (3). Sokoto: Department Of Nigerian Languagaes, Usmanu Ɗanfodiyo Uniɓersity.

Sallau, B.A. (2010). *Wanzanci da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kaduna: M.A. Najiu Professioinal Printers.

Sallau, B.A. (2013). *Wanzanci da Sauye-Sauyen Zamani*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press Limited.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 2.8 Amsoshin Tamabayoyin Auna Fahimta

1 Shin ana amfani da baki wajen sadarwa?

- Haka ne.

3. Yi bayani biyu daga cikin hanyoyin sadarwa na baki

- Murguɗa Baki
  Alamar sadarwa ce ta raini. Hanya ce da ake murguɗa leɓen ƙasa da na sama. Saƙon da ake isarwa shi ne rashin kurna ko raina wani ko wata.
- Zumɓura Baki
  Wannan hanya ce wadda ake turo leɓe gaba domin isar da wani saƙo. Idan yaro ya zumɓura baki, wannan na nuna shagwaɓa, idan kuma babban mutum ne ya yi, to wannan na nufin raini ne.
- Buɗe Baki
  Wannan hanya ce wadda ake buɗe baki ma'ana a raba leɓe sama da ƙasa domin isar da wani saƙo. Idan mutum ya buɗe baki, wannan na sadarwa ta mamaki, idan kuma babban mutum ya buɗe baki, to wannan na nufin mamaki.
- Gwalo
  Ana yin gwalo ne ta hanyar gwale idanu tare da zaro harshe waje a kalli wanda ake yi wa. Akan yi gwalo ne domin muzantawa. Yawanci an fi yi wa wanda aka raina. Haka kuma isharar gwalo ta fi faruwa a tsakanin abokai ko kuma yara su yi wa babban gwalo.
- Zunɗe
  Irin wannan ishara da baki ake yin ta yadda ake yi shi ne akan kaikaici idon wanda za a yi wa zunɗen ne sai a kuma kalli wanda za a ba shi labarin sai masu yin zunɗen su cura bakunansu gaba ana yi ana dawowa da shi gaba da baya ana nuna wanda ake zunɗe ana ɗan gantsarewa. Wannan irin ishara babu abin da da take nunawa sai munafunci da haɗa kisisinar tsiya wanda in ba a yi sa'a ba wanda ake yi wa ya gane sai rikici ya tashi. Haka kuma, mai yin zunɗe ana nuna cewar lallai mutum matsoraci ne tun da ba za ya iya fitowa ya faɗi abin da ake so game da wanda yake zunɗen ba (Adamu, 1995:26).
- Murmushi
  Sadarwa ce da ake yi domin nuna farin-ciki ko soyayya ko murna ko amincewa da juna. Ana yin wannan ishara ce ta hanyar mutum zai saki fuskarsa tare da da ɗan ɓuɗe bakinsa yadda zai fito da haƙoransa waje.

## Kashi Na Uku (3) Hanyar Sadarwa Ta Hannu

### Abubuwan Da Suke Ciki


3.1 Gabatarwa
3.2 Manufar Darasi
3.3 Hanyar sadarwa ta hannu
 3.3.1 Yin jijjina da hannu
 3.3.2 Ɗaga Hannu sama
 3.3.3 Yafice da hannu
 3.3.4 Yarfar da hannu
 .3.5 Nuna manunin yatsa
 .3.6 Nuna tafin hannu yatsu a mkiƙe
 3.3.7 Bubbuga tafukan hannu biyu
 3.3.8 Kaɗa hannu daga dama zuwa hagu tare da yatsu suna jere da juna
 3.3.9 Lissafa yatsun hannu
 Auna Fahimta
3.4 Taƙaitawa
3.5 Ma'anar wasu kalmomi
3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
3.7 Amsoshin Auna Fahinta


### 3.1 Gabatarwa

Wannan kashi ne da ya yi bayanin shafe wasali a wasu kalmomi sakamakon wasu dalilai. Wannan ɓangare ya sha bamban da wanda ya gabata domin wancan ya yi magana akan saƙalawa ma'ana ƙarawa, wannan kuma ya yi magana ne akan shafewa ma'ana ragewa. Abu ne sananne a Hausa a sami wasu kalmomi a ji ana furta su ba kamar yadda suke a rubuce ba, kuma hakan ba ya sauya ma'anar kalma daga ma'narta ta asali. Mafi yawa hakan na faruwa ne domin neman sauƙin furuci, to amma tunda manufar magana shi ne a fahimci saƙo, hakan bai saɓa ba. Akwai wurare da dama da ake samun shafe wasali kamar yadda aka kawo su a wannan kashi.

### 3.2 Manufar Darasi

A ƙarshen darasi ana sa ran dalibai za su iya:

- Fahimtar shafe wasali.
- Fahimtar dalilan shafe wasali.
- Gano sassan kalma da ake shafe wasali.

## 3.3 Hanyar Sadarwa ta hannu

Hausawa suna amfani da hannu ko hannuwansu a wajen isar da saƙo ta hanyar yin nuni a madadin magana ta fatar baki. Ana amfani da hannu wajen isar da saƙonni da dama da suka haɗa da gaisuwar ban-girma, gargaɗi, amincewa, kira, tuhuma, kore abu da sauransu. Saƙonnin sun haɗa da:

### 3.3.1 Yin jijjina da hannu

Hanya ce ta isar da saƙo wanda ake aiwatar da ita ta hanyar amfani da hannu. Idan Bahaushe ya dunƙule yatsunsa ya ɗaga hannu sama, ya jijjina, to yana nufin gaisuwa tare da girmamawa. Mutane masu alfarma ake yi wa irin wannan gaisuwa kamar sarakuna da sauransu.

### 3.3.2 Ɗaga Hannu sama

Haka ma, akwai hanyar sadarwa ta amfani da ɗaga hannu. Idan Bahaushe ya ɗaga hannunsa sama, sannan ya saki yatsunsa biyar, ya kaɗa hannun daga dama zuwa hagu, to yana nufin yana yi maka fatan alheri, kamar a ce a dawo lafiya.

### 3.3.2 Yafice da hannu

Yafice da hannu ita ma hanya ce wadda ake amfani da ita wajen isar da saƙo. Bahaushe yana amfani da hannun wajen kira. Idan Bahaushe ya miƙar da yatsunsa biyar a haɗe, sannan ya riƙa yafato iska, to yana nufin mutumin da yake nesa da shi ya zo.

### 3.3.3 Yarfar da hannu

Ita kuwa yarfar da hannu, hanya ce da Hausawa suke amfani da ita wajen isar da saƙo. Idan Bahaushe ya miƙar da hannunsa, sannan kuma ya riƙa yarfar da hannun daga ƙasa zuwa sama, to wannan yana nufin a tafi a bashi guri/kora; wato dai, yana korarka ne daga wurin. Haka idan Bahaushe ya riƙa yarfar da hannunsa da sauri da sauri babu ƙaƙƙautawa wannan ya nuna ya jin raɗaɗi ko ko jin zafi/ciwo kan abun da aka yi masa.

### 3.3.4 Nuna manunin yatsa

Ta hanyar nuna manunin yatsa, Hausawa suan ana amfani da ita wajen isar da saƙo. Idan Bahaushe ya miƙar da ɗan yatsansa (Manuni), sannan

ya dunƙule sauran guda huɗun, sai kuma ya riƙa karkaɗa yatsan dake miƙe, to yana ja maka kunne kenan ko gashedi.

**3.3.6 Nuna tafin hannu yatsu a mkiƙe**

Sannnan idan Bahaushe ya ɗaga tafin hannunsa ya nuna maka, sannan kuma yatsunsa biyar aware, to yana zagi kenan. Wannan shi ake kira daƙuwa.

**3.3.7 Bubbuga tafukan hannu biyu**

Idan Bahaushe ya miƙar da tafukansa biyu yana bubbuga su a hankali kamar yana tafi, to yana nufin ya gode, ko sannu ko kuma babu komai ko muna tare. Amma shi muna tare haɗe su ake yi na na ɗan lokaci.

**3.3.8 Kaɗa hannu**

Kaɗa hannu daga dama zuwa hagu tare da yatsu suna jere da juna.Idan Bahaushe ya miƙar da yatsunsa alhali suna jere da juna, sannan ya riƙa kaɗa hannun daga dama zuwa hagu, to yana nufin mutum bashi da hankali ko zagin ƙasƙanci:

**3.3.9 Lissafa yatsun hannu**

Bahaushe yana nuna yatsa a maimakon adadi. Misali, yatsa ɗaya ga lamba ɗaya, yatsu biyu lamba biyu, haka-haka. Idan kuma Bahaushe ya kaikaita tafin hannunsa, yatsun a miƙe sannan ya giciya shi a tsakiyar ɗayan to wannan yana nufin rabi.

**Auna Fahimta na 1**

1. Me ka fahinta da sadarwar hannu?
2. Yi bayani kan huɗu daga cikin ire-iren hanyoyin isar da saƙo na hannu

## 3.4 Taƙaitawa

A wannan kashi an koyi abubuwa kamar su:

i. Ma'anar sadarwa ta hannu
ii. Ire-iren sadarwa ta hannu
iii. Yadda ake gudanar da sadarwa ta hannu

## 3.5 Ma'anar Wasu Kalmomi

Yarfar da: - na nufin a tafi a bashi guri/kora.
Yafice da hannu: - yana nufin mutumin da yake nesa ya zo ma'ana kiran mutumin da ake a nesa.

## 3.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

CNHN, (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity press.

Lawal, N. da Adamu, H.B. (2020). Saayee A Wasu Sassan Jiki a Al'adun Hausawa. In *Ɗaunɗaya Journal of Hausa Studies,* Ɓol.2 (3). Sokoto: Department Of Nigerian Languagaes, Usmanu Ɗanfodiyo Uniɓersity.

Sallau, B.A. (2010). *Wanzanci da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kaduna: M.A. Najiu Professioinal Printers.

Sallau, B.A. (2013). *Wanzanci da Sauye-Sauyen Zamani*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press Limited.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 3.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Me ka fahinta da sadarwar hannu?
   Hausawa suna amfani da hannu ko hannuwansu a wajen isar da saƙo ta hanyar yin nuni a madadin magana ta fatar baki. Ana amfani da hannu wajen isar da saƙonni da dama da suka haɗa da gaisuwar ban-girma, gargaɗi, amincewa, kira, tuhuma, kore abu da sauransu.
2. Yi bayani kan huɗu daga cikin ire-iren hanyoyin isar da saƙo na hannu

i- Yin jijjina da hannu
Idan Bahaushe ya dunƙule yatsunsa ya ɗaga hannu sama, ya jijjina, to yana nufin gaisuwa tare da girmamawa. Mutane masu alfarma ake yi wa irin wannan gaisuwa kamar sarakuna da sauransu.

ii- Ɗaga Hannu sama
Idan Bahaushe ya ɗaga hannunsa sama, sannan ya saki yatsunsa biyar, ya kaɗa hannun daga dama zuwa hagu, to yana nufin yana yi maka fatan alheri, kamar a ce a dawo lafiya.

iii- Yafice da hannu
Bahaushe yana amfani da hannun wajen kira. Idan Bahaushe ya miƙar da yatsunsa biyar a haɗe, sannan ya riƙa yafato iska, to yana nufin mutumin da yake nesa da shi ya zo.

**Iɓ- Yarfar da hannu**

Idan Bahaushe ya miƙar da hannunsa, sannan kuma ya riƙa yarfar da hannun daga ƙasa zuwa sama, to wannan yana nufin a tafi a bashi guri/kora; wato dai, yana korarka ne daga wurin. Haka idan Bahaushe ya riƙa yarfar da hannunsa da sauri da sauri babu ƙaƙƙautawa wannan ya nuna ya jin raɗaɗi ko ko jin zafi/ciwo kan abun da aka yi masa.

ɓ- Nuna manunin yatsa Idan Bahaushe ya miƙar da ɗan yatsansa (Manuni), sannan ya dunƙule sauran guda huɗun, sai kuma ya riƙa karkaɗa yatsan dake miƙe, to yana ja maka kunne kenan ko gashedi.

ɓi- Nuna tafin hannu yatsu a mkiƙe
Idan Bahaushe ya ɗaga tafin hannunsa ya nuna maka, sannan kuma yatsunsa biyar aware, to yana zagi kenan. Wannan shi ake kira daƙuwa.
ɓii- Bubbuga tafukan hannu biyu

Idan Bahaushe ya miƙar da tafukansa biyu yana bubbuga su a hankali kamar yana tafi, to yana nufin ya gode, ko sannu ko kuma babu komai ko muna tare. Amma shi muna tare haɗe su ake yi na na ɗan lokaci.

ɓiii- Kaɗa hannu daga dama zuwa hagu tare da yatsu suna jere da juna

Idan Bahaushe ya miƙar da yatsunsa alhali suna jere da juna, sannan ya riƙa kaɗa hannun daga dama zuwa hagu, to yana nufin mutum bashi da hankali ko zagin ƙasƙanci:

## Kashi Na Huɗu (4) Hanyar Sadarwa Ta Ido

### Abubuwan Da Suke Ciki


4.1 Gabatarwa
4.2 Manufar Darasi
4.3 Hanyar sadarwa ta Ido
  4.3.1 Ƙifce
  4.3.2 Kanne
  4.3.3 Zare Ido
  4.3.4 Linshe Ido
  4.3.5 Rintse Ido
  Auna Fahimta
4.4 Taƙaitawa
4.5 Ma'anar wasu kalmomi
4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
4.7 Amsoshin Auna Fahinta


### 4.1 Gabatarwa

Wannan kashi ya yi bayanin hanyar sadarwa ta amfani da ido. Kamar yadda abin ya nuna hanya ce da ake isar saƙo da ido ta mabambanta hanyoyi. An kawo bayani kan nau'o'in isar da saƙo ta hanyar sadarwa ta gargajiya wadda ta shafi ido. Bugu da ƙari wannan kashi ya kawo misalai don ƙara fahimta.

### 4.2 Manufar Darasi

A ƙarshen darasi ana sa ran dalibai za su iya:

- Fahimtar hanyar sadarwa ta ido.
- Fahimtar ire-iren sadarwa ta ido
- Bambance ire-iren sadarwa ta ido.

### 4.3 Hanyar sadarwa ta Ido

Hnayar sadarwa ta ido wata hanya ce da Bahaushe yake amfani da ita wajen isar da saƙo wanda ya shafi ko yake bayyana soyayya, shagwaɓa, dakatarwa, da sauransu. An kan yi amfani da ido wajen isar da saƙonni.

### 4.2.1 Ƙifce

Alama ce ta jan hankali ko kuma dakatarwa. Idan mutum yana cikin magana a muhallin da ba damar a ce da shi bari, sai a ƙifta masa ido sau ɗaya domin dakatar da shi daga cigaba da wannan zance da yake yi.

Mafi yawancin lokaci, ana dakatar da mutum daga zance ta hanyar ƙifce idan ya zama yana faɗin maganar da bata dace ba game da wani mutum sai kuma ya zama shi mutumin ko wani nasa ya bayyana a wajen ba tare da sanin mai maganar ba, ko ma idan aka tsinkayo wani makusancin wanda ake maganar a kansa yana dosowa, to sai a ƙiftawa mai magana ido domin ya dakata da maganar.

Shi kuwa ƙifce ana yinsa ne ta hanyar rufe idanuwa biyu a buɗe sau ɗaya a hankali.

### 4.3.5 Kanne

Kanne shi ne a rufe ido ɗaya sannan a buɗe shi da sauri-da-sauri tare kuma da ɗan karkatar da kai ta gefen idon da aka yi kannen da shi. Ana yin kanne domin ankararwa.

### 4.3.6 Zare Ido

Bahaushe kan zaro idanuwansa gwala-gwala ko dara-dara domin nuna halin tsoro musamman lokacin da ya yi arba da wani abin tsoro kamar wata dabba da sauransu.

### 4.3.7 Linshe Ido

Bahaushe na nuna kunya da kuma ƙasƙantar da kai ta hanyar linshe idanu, sannan a sunkuyar da kai ƙasa. Shi linshe ido shi ne rufe idanu amma ba rif ba. Sannan kuma a wasu lokutan linshe idon na nuna alamun barci. Shi kuwa linshe idanun barci ana gane shi ne idan ya zama mutum ya linshe idanun sannan yana yin ɗan layi ko kuma yana magana yana katsewa ko kuma yana hamma.

### 4.3.5 Rintse Ido

Bahaushe yana rintse idanunsa domin nuna tausayi. Shi kuma rintse ido shi ne mutum ya rufe idanuwansa da bakinsa a lokaci guda tare da yamutse fuska. Misali, idan Bahaushe ya ga ana tsattsaga jikin yaro, yakan rintse idanuwansa da nufi cewa baya son ganin zubar jinin da kuma kukan da yaron yake yi sai ya rintse ido.

**Auna Fahimta na 1**

| |
|---|
| Me ake nufi da rintse ido?<br>Kawo huɗu daga cikin nau'o'in sadarwa ta ido |

## 4.4 Taƙaitawa

A wannan kashi an koyi abubuwa kamar haka:

- Hanyar sadarwa ta ido.
- Ire-iren sadarwa ta ido.

## 4.5 Ma'anar Wasu Kalmomi

gwala-gwala ko dara-dara: buɗe ido
rintse ido: shi ne mutum ya rufe idanuwansa da bakinsa a lokaci guda tare da yamutse fuska.

## 4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari


Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

CNHN, (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity press.

Lawal, N. da Adamu, H.B. (2020). Saayee A Wasu Sassan Jiki a Al'adun Hausawa. In *Ɗaunɗaya Journal of Hausa Studies,* Ɓol.2 (3). Sokoto: Department Of Nigerian Languagaes, Usmanu Ɗanfodiyo Uniɓersity.

Sallau, B.A. (2010). *Wanzanci da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kaduna: M.A. Najiu Professioinal Printers.

Sallau, B.A. (2013). *Wanzanci da Sauye-Sauyen Zamani*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press Limited.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. Me ake nufi da rintse ido?

Shi ne mutum ya rufe idanuwansa da bakinsa a lokaci guda tare da yamutse fuska. idan Bahaushe ya ga ana tsattsaga jikin yaro, yakan rintse idanuwansa da nufi cewa baya son ganin zubar jinin da kuma kukan da yaron yake yi sai ya rintse ido.

2.Kawo huɗu daga cikin nau'o'in sadarwa ta ido.

i. Ƙifce

Alama ce ta jan hankali ko kuma dakatarwa. Idan mutum yana cikin magana a muhallin da ba damar a ce da shi bari, sai a ƙifta masa ido sau ɗaya domin dakatar da shi daga cigaba da wannan zance da yake yi.

ii. Kanne

Kanne shi ne a rufe ido ɗaya sannan a buɗe shi da sauri-da-sauri tare kuma da ɗan karkatar da kai ta gefen idon da aka yi kannen da shi. Ana yin kanne domin ankararwa.

iii. Zare Ido

Bahaushe kan zaro idanuwansa gwala-gwala ko dara-dara domin nuna halin tsoro musamman lokacin da ya yi arba da wani abin tsoro kamar wata dabba da sauransu.

iv. Linshe Ido

Bahaushe na nuna kunya da kuma ƙasƙantar da kai ta hanyar linshe idanu, sannan a sunkuyar da kai ƙasa. Shi linshe ido shi ne rufe idanu amma ba rif ba. Sannan kuma a wasu lokutan linshe idon na nuna alamun barci. Shi kuwa linshe idanun barci ana gane shi ne idan ya zama mutum ya linshe idanun sannan yana yin ɗan layi ko kuma yana magana yana katsewa ko kuma yana hamma.

Ɓ. Rintse Ido

Bahaushe yana rintse idanunsa domin nuna tausayi. Shi kuma rintse ido shi ne mutum ya rufe idanuwansa da bakinsa a lokaci guda tare da yamutse fuska.

## Kashi Na Biyar (5) Hanyar Sadarwa Ta Haɗaka

### Abubuwan Da Suke Ciki

5.1 Gabatarwa
5.2 Manufar Darasi
5.3 Hanyar sadarwa ta Haɗaka
 5.3.1 Fuska da hannu da ido
 5.3.2 Hannu da kunne
 5.3.3 Yatsa da Kunne
 5.3.4 Yatsan dama da hagu
 5.3.5 Tsinin harshe da yatsa
 5.3.6 Tsinin harshe da yatsa da baki
 5.3.7 Kunci da yatsa
 5.3.8 Yatsun hannu da baki
 5.3.9 Fuska da tafin hannu
 5.3.10 Tafin hannun da manuni da babban yatsa
 5.3.11 Baki da manuni
 5.3.12 Tafin hannu da ƙofar hanci.
 5.3.13 Hannu da kafaɗa ko ciki
 5.3.14 Hannaye da ka
 Auna Fahimta
5.4 Taƙaitawa
5.5 Ma'anar wasu kalmomi
5.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
5.7 Amsoshin Auna Fahinta



### 5.1 Gabatarwa

Wannan kashi ya yi bayanin hanyar sadarwa ta amfani da wasu sassa. Kamar yadda abin ya nuna hanya ce da ake isar saƙo ta hanyar haɗa wata gaɓa ko wani sashi na jiki wajen isar da saƙo ga wani ko wata ko ma wasu. An kawo bayani kan nau'o'in isar da saƙo ta hanyar sadarwa ta gargajiya wadda ta shafi haɗakar gaɓoɓi. Bugu da ƙari wannan kashi ya kawo misalai don ƙara fahimta.



### 5.2 Manufar Darasi

A ƙarshen darasi ana sa ran dalibai za su iya:

- Fahimtar hanyar sadarwa ta haɗaka.
- Fahimtar ire-iren sadarwa ta haɗaka
- Bambance ire-iren sadarwa ta haɗaka.

## 5.3 Hanyar sadarwa ta Haɗaka

Bahaushe kan gauraya gaɓoɓinsa a wasu lokutan idan aka samu yanayin da gaɓa guda bata isa ba wajen sadarwa. Irin wannan sadarwa ta haɗaka, Hausawa kan yi amfani da wasu sassa domin isar da saƙo, kamar haɗa hannu da hanci a wajen yin guɗa da sauransu. Misali, idan Bahaushe yana son ya ce da kurma "tafi ka dawo gobe". Sai ya miƙar da hannunsa, sannan ya kaɗa shi gaba, sai kuma ya karkatar da kansa zuwa kafaɗarsa, sai kuma ya tallabi kan da tafin hannunsa tare da linshe idanuwansa. Wannan shi ne ke nuna waccar maganar da muka faɗa a sama. Ga kaɗa daga cikin irin waɗannan alamomi na sadarwa.

### 5.6.1 Fuska da hannu da ido

Awannan hanya Hausawa suna amfani da fuska da hannu da ido wajen isar da saƙo. Idan aka ɗora fuska a kan tafin hannu tare da linshe idanuwa, wannan sadarwa ce wadda take nufin ji ko yin barci.

### 5.6.2 Kunne da Hannu

Wannan hanya ce da Hausawa suke amfani da ita domin isar da saƙo. A irin wannan a kan riƙe jefin kunne ta ƙasa sannan a jijjiga kunnen, wanda yin hakan na nufin isar da saƙo na gargaɗi.

### 5.6.3 Yatsa da Kunne

Wannan ma hanya ce wadda Hausawa suke amfani da ita wajen isar da saƙo. A wannan hanyar ana ɗora yatsa a kunne sannan a kewaya bayan kunnen da shi, wanda hakan ke isar da saƙo na ƙaryata magana ko wani abu.

### 5.6.4 Hannu da hannu

A irin wannan sadarwa ta isar da saƙo, ana aiwatar da ita ne ta hanyar karkaɗa yatsu biyu manuni na hannun dama da hagu sannan yi sama da ƙasa a saɓe, ma'ana ba tare ba. Wannan na nuna alamar gudu.

### 5.6.5 Tsinin harshe da yatsa

Hauasawa suna isar da saƙo ta hanyar amfani da tsinin harshe da yatsa. A wannan sadarwa yatsa yakan taɓa tsinin harshe. Irin wannan sadarwa na nufin ɗanɗano.

### 5.6.6 Tsinin harshe da yatsa

Ita ma wannan sadarwa ana aiwatar da ita hanyar taɓa tsinin harshe da yatsa ɗaya sannan a furzar, wannan sadarwa ce wadda take nufin ɗaci na wani abu.

### 5.6.7 Kunci da Yatsa

Ana isar da saƙo ta amfani da zozar kunci da yatsa ɗaya na nufin daɗi ko zaƙi.

### 5.6.8 Yatsu baki

Ita kuma sadarwar da ake yi ta amfani da yatsu da baki. A wannan irin sadarwa ana yin ta ta hanyar tsuke yatsun hannun dama sannan a riƙa kai su baki. Wannan na isar da saƙon cin abinci.

### 5.6.9 Fuska da tafin hannu

Ana irin wannan sadarwa ta hanyar ɗora fuska a tafin hannu, sannan a ɗaga a kuma nuna baya da babban yatsa sau ɗaya, wannan na nufin jiya. Sau biyu kuma shekaran jiya.

### 5.6.10 Tafin hannu da manunin yatsa

Wannan sadarwa ce wadda ake miƙar da tafin hannun hagu sannan a riƙa cusa shi tsakanin manuni da babban yatsan hannun dama wannan na nufin ƙirgar kuɗi.

### 5.6.11 Baki da yatsa (manuni)

Ana yin irin wannan sadarwa ta hanyar rufe baki, sannan a ɗora manuni a tsakiyar bakin wannan na nufin a yi shiru.

### 5.6.12 Tafin hannu da hanci

Idan aka ɗora tafin hannu a ƙofar hanci ana shinshinawa na nufin isar da saƙo mai nuna ƙanshi.

### 5.6.13 Hannu da wani sashe na jiki

Idan aka yi amfani da hannu aka sosa wani sashe na jiki, wannan saƙo ne da ke nufin ƙaiƙayi.

### 5.6.14 Hannaye da kai

Hausawa suan isar da saƙo mai nuna damuwa ta hanyar ɗora hannaye biyu a ka.

**Auna Fahimta na 1**

1.Ta ya ya ake gane sadarwa mai nuna cin abinci?
2.Kawo huɗu daga cikin nau'o'in sadarwa ta haɗaka

## 4.4 Taƙaitawa

A wannan kashi an koyi abubuwa kamar haka:

- Hanyar sadarwa ta haɗaka.
- Ire-iren sadarwa ta haɗaka.

## 4.4 Ma'anar Wasu Kalmomi

- Shiru – daina yin magana
- Ƙaiƙayi – wani abu da ake sanyawa a sosa jiki.

## 4.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

CNHN, (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity press.

Lawal, N. da Adamu, H.B. (2020). Saayee A Wasu Sassan Jiki a Al'adun Hausawa. In *Ɗaunɗaya Journal of Hausa Studies*, Ɓol.2 (3). Sokoto: Department Of Nigerian Languagaes, Usmanu Ɗanfodiyo Uniɓersity.

Sallau, B.A. (2010). *Wanzanci da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kaduna: M.A. Najiu Professioinal Printers.

Sallau, B.A. (2013). *Wanzanci da Sauye-Sauyen Zamani*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press Limited.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 4.7 Amsoshin Tambayoyin Auna Fahimta

1. .Ta ya ya ake gane sadarwa mai nuna cin abinci?
   Ita kuma sadarwar da ake yi ta amfani da yatsu da baki. A wannan irin sadarwa ana yin ta ta hanyar tsuke yatsun hannun dama sannan a riƙa kai su baki. Wannan na isar da saƙon cin abinci.
2. Kawo huɗu daga cikin nau'o'in sadarwa ta haɗaka tare da bayani

i- Fuska da hannu da ido
Awannan hanya Hausawa suna amfani da fuska da hannu da ido wajen isar da saƙo. Idan aka ɗora fuska a kan tafin hannu tare da linshe idanuwa, wannan sadarwa ce wadda take nufin ji ko yin barci.

ii- Kunne da Hannu
Wannan hanya ce da Hausawa suke amfani da ita domin isar da saƙo. A irin wannan a kan riƙe jefin kunne ta ƙasa sannan a jijjiga kunnen, wanda yin hakan na nufin isar da saƙo na gargaɗi.

iii- Yatsa da Kunne
Wannan ma hanya ce wadda Hausawa suke amfani da ita wajen isar da saƙo. A wannan hanyar ana ɗora yatsa a kunne sannan a kewaya bayan kunnen da shi, wanda hakan ke isar da saƙo na ƙaryata magana ko wani abu.

Iɓ- Hannu da hannu
A irin wannan sadarwa ta isar da saƙo, ana aiwatar da ita ne ta hanyar karkaɗa yatsu biyu manuni na hannun dama da hagu sannan yi sama da ƙasa a saɓe, ma'ana ba tare ba. Wannan na nuna alamar gudu.

ɓ- Tsinin harshe da yatsa
Hauasawa suna isar da saƙo ta hanyar amfani da tsinin harshe da yatsa. A wannan sadarwa yatsa yakan taɓa tsinin harshe. Irin wannan sadarwa na nufin ɗanɗano.

ɓi- Tsinin harshe da yatsa
Ita ma wannan sadarwa ana aiwatar da ita hanyar taɓa tsinin harshe da yatsa ɗaya sannan a furzar, wannan sadarwa ce wadda take nufin ɗaci na wani abu.

ɓii- Kunci da Yatsa
Ana isar da saƙo ta amfani da zozar kunci da yatsa ɗaya na nufin daɗi ko zaƙi.

ɓiii- Yatsu baki
Ita kuma sadarwar da ake yi ta amfani da yatsu da baki. A wannan irin sadarwa ana yin ta ta hanyar tsuke yatsun hannun dama sannan a riƙa kai su baki. Wannan na isar da saƙon cin abinci.

iɗ- Fuska da tafin hannu

Ana irin wannan sadarwa ta hanyar ɗora fuska a tafin hannu, sannan a ɗaga a kuma nuna baya da babban yatsa sau ɗaya, wannan na nufin jiya. Sau biyu kuma shekaran jiya.

## RUKUNI NA HUƊU (4) HANYOYIN SADARWA TA ZAMANI

Kashi Na 1 Sadarwa ta Zamani
Kashi Na 2 Muhimmancin Sadarwa

### Kashi Na 1 Sadarwa Ta Rediyo

**Abubuwan da Suke Ciki**

1.1 Gabatarwa
1.2 Manufar Darasi
1.3 Sadarwa ta zamani
 1.3.1 Sadarwa ta rediyo
 1.3.2 Sadarwa ta Talbijin
 1.3.3 Sadarwa ta Jarida
 1.3.4 Sadarwa wayar hannu
 Auna Fahimta
1.4 Taƙaitawa
1.5 Ma'anar wasu kalmomi
1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
1.7 Amsoshin Auna Fahinta



### 1.1 Gabatarwa

A wannan kashi an yi bayani kan yadda ake aiwatar da sadarwa ta hanyar zamani. Sannan an kawo ire-irensa sadarwa ta zamani da ake amfani da wata na'ura wajen isar da saƙo. Amma yana da kyau mu fahimci cewa, sadarwa ta zamani na ɗaya daga cikin ire-iren sadarwa da ake amfani da ita a yau. Sannan an kawo bayanai kan sadarwa ta zamani.



### 1.2 Manufar Darasi

Bayan kammala wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Bayani a kan ire-iren sadarwa ta zamani.
- Bayyana sadarwa ta rediyo.
- Bayyana sadarwa ta talbijin
- Bayyana sadarwa ta jarida
- Bayyana ƙafofin sadarwa na zamani

## 1.3 Sadarwa ta zamani

Wata kafa da take yin amfani da harshen ɗan'adam ta hanyar furuci ko rubutu don isar da saƙo ga al'umma a lokaci guda ta hanyar amfani da wata na'ura. Irin wannan hanyar sadarwa kamar yadda aka bayani tunda farko akwai ta rediyo da talabijin da sadarwa ta jarida da kuma wayar tafi da gidanka (waya) da sauransu. Yanzu za aka kawo bayani daki-daki kan hanyar sadarwa ta zamani.

### 1.3.1 Rediyo

Rediyo kafa ce ta sadarwa wadda muhimmiyar hanya ce ta sadarwa wadda ake yin amfani da da na'ura wajen isar da saƙo ga al'umma. Ita kafar sadarwa ce da ba ta yin amfani da hoto, murya ita aka fi ji. Wato hanya ce da isar da saƙo ga ɗimbin al'umma cikin sauƙi kuma a lokaci guda. koyaushe masu sauraro suke jin shirye-shirye ta hanyar amfani da harshen ɗan'adam, musamman ta hanyar furuci tare da amfanin na'ura. A dunƙule dai, ka sani cewa sai mutum ya mallaki na'urar rediyo sannan zai iya jin wani saƙo cikin wani harshe. Kuma wannan ita ce hanya mafi sauƙi ga kowa a kan sauran kafofin na talabijin da na jarida. Shi ya sa daga rukuni na gaba duk bayanan da zan yi maka dangane da Hausa a kafofin watsa labarai ya danganci kafar sadarwa ta rediyo.

### 13.2 Talabijin

Talabijin kafar sadarwa ce da take isar da saƙo ta hanyar amfani da murya da hoto. Kafar sadarwa ta talabijin tana yin amfani da harshe ta yin furuci ko ta yin rubutu haɗe da nuna hoto don isar da saƙo. A irin wannan kafa mutum ba zai samu wani saƙo ba face sai ya mallaki talabijin tare da wasu na'urori da za su taimaka ya iya ganin hoto da jin murya. Ka ga irin wannan kafa ba kowa ne yake da ikon mallakarta ba sai wnda yake da hali ko sukunin sayen talabijin. Talabijin a yau ta zama ruwan dare musamman a manyan birane.

### 1.3.3Jarida

Kafar sadarwa ta jarida ita ma tana taka rawa wajen isar da saƙo. Idan ka duba tarihin bunƙasa da yaɗuwar harshen Hausa za ka ga cewa jarida ta bayar da gudummawa ta a zo a gani. Ba kowa ne yake iya samun ko mallakar jarida ba, domin sai an sa kuɗi kafin a same ta a karanta har a ji saƙon da take ɗauke da shi. Bugu da ƙari, ita jarida tana fitowa ne kowace rana, wasu kuma suna fitowa sau ɗaya ko sau biyu a mako.

### 1.3.4 Wasu Kafofin Sadarwa na Zamani

Sai kuma wannan hanya wadda ta shafi sadarwa ta zamani ko hanyar isar da saƙo ga al’umma masu yawa a lokaci guda. Irin waɗannan hanyoyin isar da saƙo ana kira su da sunan zamani saboda zamani na duniya a tafin hannu shi ya kawo su ko kuma shirin game duniya wanda ya haifar da su. Waɗannan kafofin sadarwa na zamani sun ƙunshi *facebook* da *WhatsApp* da *Instagram* da *Twitter* da sauransu. A irin waɗannan kafafe ana yin amfani da wayar hannu ko kwamfuta wajen isar da saƙo ta hanyar furuci ko rubutu. A kafofin sadarwa na zamani kowa ma yana da damar faɗin albarkacin bakinsa ya watsa ga rukunin jama’a. A ƙasashe da dama kafofin sadarwa na zamani ba sa bisa wasu dokoki ko sharuɗɗa na ƙasa. Saboda ana yin amfani da waya lokaci guda labari yake isa ga kowa saɓanin rediyo da talabijin da kuma jarida waɗanda sai an tace saƙon da za a aika.

**Auna Fahimta**

1. Me ake nufi da sadarwa ta zamani?
2. Yi bayani biyu daga cikin hanyoyin sadarwa na zamani

## 1.4 Taƙaitawa

A wannan darasin an koyi abubuwa kamar haka:
i. Ma'anar sadarwa ta zamani
ii. Ire-iren sadarwa ta zamani

## 1.5 Ma’anar Wasu Kalmomi

Rediyo – wata na’ura ce da ake amfani da ita wajen isar da saƙo wadda za a iya ji
Talbijin – wata na’ura ce da ake amfani da ita wajen isar da saƙo wadda za a ji a gani

## 1.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

CNHN, (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami’ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity press.

Lawal, N. da Adamu, H.B. (2020). Saayee A Wasu Sassan Jiki a Al’adun Hausawa. In Ɗ*aunɗaya Journal of Hausa Studies,* Ɓol.2 (3). Sokoto: Department Of Nigerian Languagaes, Usmanu Ɗanfodiyo Uniɓersity.

Sallau, B.A. (2010). *Wanzanci da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kaduna: M.A. Najiu Professioinal Printers.

Sallau, B.A. (2013). *Wanzanci da Sauye-Sauyen Zamani.* Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity Press Limited.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniɓersity Press PLC.

## 1.7 Amsoshin Tamabayoyin Auna Fahimta

1. Me ake nufi da sadarwa ta zamani?

Wata kafa da take yin amfani da harshen ɗan'adam ta hanyar furuci ko rubutu don isar da saƙo ga al'umma a lokaci guda ta hanyar amfani da wata na'ura. Irin wannan hanyar sadarwa kamar yadda aka bayani tunda farko akwai ta rediyo da talabijin da sadarwa ta jarida da kuma wayar tafi da gidanka (waya) da sauransu. Yanzu za aka kawo bayani daki-daki kan hanyar sadarwa ta zamani.

2.Yi bayani biyu daga cikin hanyoyin sadarwa na zamani

**i- Rediyo**

Rediyo kafa ce ta sadarwa wadda muhimmiyar hanya ce ta sadarwa wadda ake yin amfani da da na'ura wajen isar da saƙo ga al'umma. Ita kafar sadarwa ce da ba ta yin amfani da hoto, murya ita aka fi ji. Wato hanya ce da isar da saƙo ga ɗimbin al'umma cikin sauƙi kuma a lokaci guda. koyaushe masu sauraro suke jin shirye-shirye ta hanyar amfani da harshen ɗan'adam, musamman ta hanyar furuci tare da amfanin na'ura. A dunƙule dai, ka sani cewa sai mutum ya mallaki na'urar rediyo sannan zai iya jin wani saƙo cikin wani harshe. Kuma wannan ita ce hanya mafi sauƙi ga kowa a kan sauran kafofin na talabijin da na jarida. Shi ya sa daga rukuni na gaba duk bayanan da zan yi maka dangane da Hausa a kafofin watsa labarai ya danganci kafar sadarwa ta rediyo.

**ii- Talabijin**

Talabijin kafar sadarwa ce da take isar da saƙo ta hanyar amfani da murya da hoto. Kafar sadarwa ta talabijin tana yin amfani da harshe ta yin furuci ko ta yin rubutu haɗe da nuna hoto don isar da saƙo. A irin wannan kafa mutum ba zai samu wani saƙo ba face sai ya mallaki talabijin tare da wasu na'urori da za su taimaka ya iya ganin hoto da jin murya. Ka ga irin wannan kafa ba kowa ne yake da ikon mallakarta ba sai wnda yake da hali ko sukunin sayen talabijin. Talabijin a yau ta zama ruwan dare musamman a manyan birane.

iv- **Jarida**

Kafar sadarwa ta jarida ita ma tana taka rawa wajen isar da saƙo. Idan ka duba tarihin bunƙasa da yaɗuwar harshen Hausa za ka ga cewa jarida ta bayar da gudummawa ta a zo a gani. Ba kowa ne yake iya samun ko mallakar jarida ba, domin sai an sa kuɗi kafin a same ta a karanta har a ji saƙon da take ɗauke da shi. Bugu da ƙari, ita jarida tana fitowa ne kowace rana, wasu kuma suna fitowa sau ɗaya ko sau biyu a mako.

**Iɓ- Wasu Kafofin Sadarwa na Zamani**

Sai kuma wannan hanya wadda ta shafi sadarwa ta zamani ko hanyar isar da saƙo ga al'umma masu yawa a lokaci guda. Irin waɗannan hanyoyin isar da saƙo ana kira su da sunan zamani saboda zamani na

duniya a tafin hannu shi ya kawo su ko kuma shirin game duniya wanda ya haifar da su. Waɗannan kafofin sadarwa na zamani sun ƙunshi *facebook* da *WhatsApp* da *Instagram* da *Twitter* da sauransu. A irin waɗannan kafafe ana yin amfani da wayar hannu ko kwamfuta wajen isar da saƙo ta hanyar furuci ko rubutu. A kafofin sadarwa na zamani kowa ma yana da damar faɗin albarkacin bakinsa ya watsa ga rukunin jama'a. A ƙasashe da dama kafofin sadarwa na zamani ba sa bisa wasu dokoki ko sharuɗɗa na ƙasa. Saboda ana yin amfani da waya lokaci guda labari yake isa ga kowa saɓanin rediyo da talabijin da kuma jarida waɗanda sai an tace saƙon da za a aika

## Kashi Na 2 Muhimmancin Sadarwa

### Abubuwan da Suke Ciki

2.1 Gabatarwa
2.2 Manufar Darasi
2.3 Muhimmancin Sadarwa
  2.3.1 Muhimmancin sadarwa ta gargajiya
  2.3.2 Muhimmancin sadarwa ta zamani
  Auna fahinta
2.4 Taƙaitawa
2.5 Ma’anar wasu kalmomi
2.6 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari
2.7 Amsoshin Auna Fahinta

### 2.1 Gabatarwa

A wannan kashi an bayyana muhimmancin sadarwa ta gargajiya da ta zamani. Kowace hanyar sadarwa tana da muhimmancinta. Amma a wannan kashi ya kamata mu fahimci cewa, sadarwa ta gargajiya da ta zamani. An kawo muhimmancin sadarwar ta gargajiya da ta zamani.

### 2.2 Manufar Darasi

Bayan kammala wannan darasi ana sa ran ɗalibai su iya:

- Bayani a kan muhimmancin sadarwa.
- Bayyana sadarwa ta gargajiya.
- Kawo sadarwa ta zamani

### 2.3 Muhimmancin sadarwa

Sadarwa tana da muhimmanci ƙwarai da gaske domin takan taimaka wa mai sauro ya fahinci saƙo da aka aiko masa ko shi ya aika a ɓangaren sadarwa ta gargajiya. Amma idan sadarwa ce ta zamani ita kuma ana bin wasu hanyoyi ta hanyar amfani da wasu na’urori da tace saƙon kafin aika saƙo.

### 2.3.5 Muhimmancin sadarwa ta gargajiya

Sadarwa ta gargajiya tana da muhimmanci kwarai. Ga wasu kamar haka:

i- Sauƙin isar da saƙo

ii- Babu kashe kuɗi
iii- Bada da damar yin tambaya nan-take
iv- Ba amfani da wutar lantarki
v- Babu wata na'ura

### 2.3.6 Muhimmancin sadarwa ta Zamani

Sadarwa ta gargajiya tana da muhimmanci kwarai. Ga wasu kamar haka
i- Isar da saƙo ga mutane masu yawa a lokaci guda
ii- Samun saƙon ba tare da ganin mai isar da saƙon ba
iii- Saurin isar da saƙo
iv- Samun saƙo a rubuce
v- Isar da ta cikin hoto

**Auna Fahimta**

| |
|---|
| 1. Muhimmancin sadarwar ta gargajiya guda biyar<br>2. Muhimmancin sadarwar ta zamani guda biyar |

## 2.5 Taƙaitawa

A wannan darasin an koyi abubuwa kamar haka:
i. Muhimmancin sadarwa
ii. Muhimmancin sadarwa ta gargajiya da ta zamani

## 2.6 Ma'anar Wasu Kalmomi

Muhimmanci - amfani

## 2.7 Manazarta da Wasu Ayyukan Ƙarin Nazari

Bunza A.M. (2002). *Rubutun Hausa Yadda Yake da Yadda Ake Yin Sa Don Masu Koyo Da Koyarwa*. Lagos: Ibrash Islamic Publications Centre L.T.D.

CNHN, (2006). *Ƙamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Zaria: Ahmadu Bello Uniɓersity press.

Lawal, N. da Adamu, H.B. (2020). Saayee A Wasu Sassan Jiki a Al'adun Hausawa. In *Ɗaunɗaya Journal of Hausa Studies,* Ɓol.2 (3). Sokoto: Department Of Nigerian Languagaes, Usmanu Ɗanfodiyo Uniɓersity.

Sallau, B.A. (2010). *Wanzanci da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kaduna: M.A. Najiu Professioinal Printers.

Sallau, B.A. (2013). *Wanzanci da Sauye-Sauyen Zamani*. Zaria: Ahmadu Bello Uniƃersity Press Limited.

Zarruƙ R. M., da Wasu (2011). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Ƙananan Makarantun Sakandire Littafi na Ɗaya*. Ibadan: Uniƃersity Press PLC.

## 2.8 Amsoshin Tamabayoyin Auna Fahimta

1. Muhimmancin sadarwar ta gargajiya guda biyar

i- Sauƙin isar da saƙo
ii- Babu kashe kuɗi
iii- Bada da damar yin tambaya nan-take
iv- Ba amfani da wutar lantarki
v- Babu wata na'ura

2. Muhimmancin sadarwar ta zamani guda biyar

i- Isar da saƙo ga mutane masu yawa a lokaci guda
ii- Samun saƙon ba tare da ganin mai isar da saƙon ba
iii- Saurin isar da saƙo
iɓ- Samun saƙo a rubuce
ɓ- Isar da ta cikin hoto